A b'angaren Rahul kuwa shi ma ya jone shi da Esta don har having sex suke,in bai je chambre d'inta ba da kanta take tardo shi can room na su.Babu tsoron Allah haka za su shige bargo su yi ta aikata masha'ar su ko kunya babu dan wani lokaci a gaban Nur su ke yi........
[11/10 à 16:44] MRS SADAUKI 💫: *MUTUM DA RIGAR ALJAN*👹

*Gajeren labari...*
Story
and
Written by
*MRS SADAUKI💫✍🏻*
{Cham rose💞}
Dedicated to *PRINCESS AYSHATOU*

☀️ *FIRST CLASS WRITTERS ASSOCIATIONS*☀️

---

BISMILLAHI RAHMANI RAHIM.

Page 16-17

Tun da Maryam ta fara rubuta ba ta tsaya ba har sai da ta kammala ta ba mushen su,waje ta fita ta zauna 'kar'kashin bishiyar mangoro dan jiran 'kawayenta.

Wani santalelen hannu ta gani an zuro mata, d'aga kai ta yi dan ganin mamallakin hannun,William ne a tsaye ya na sakar mata murmushi.Ba tayi wani tunani ba ta d'ora hannunta akan nasa nan ya ja su izuwa wata duniya mai cike da ciyayi da shubke-shubke,cike da murna ta fizge hannunta tare da rugawa wurin da ruwa ke kwaranya ta jikin wasu duwatsu,ko kafin ta 'karasa kayan jikinta sun canza zuwa riga da wando 'kananu masu masifar kyau.

Lumshe ido ta yi ta na fitar da wani numfashi wanda ke nuni ta na son yanayin,ribob d'in kanta ya cire nan sumar kanta ta baje bisa kafad'unta yayin da William ya rungumeta ta baya ya na mai zagayo hannayen shi bisa shatin cikinta.

"You like this baby?" ya fada ya na mai d'ora kan shi bisa wuyanta,ba ta ce komai ba sai juyowa da tayi su na facing juna ta na mai kallon boules ɗin idonsa uwanda suke matukar burgeta .Janyota yayi izuwa inda ruwan ke zuba sosai,saurin 'kankame shi ta yi ta na mai fitar da kanta daga ruwan dan samun damar shed'awa alama kawai yayi da hannu nan take ruwan suka bar sauka a kanta sai a jiki.

Sai da su ka yi wanka sosai sannan suka fito,bisa wani gadon flower su ka zauna wanda a gefen shi kuma wani d'an d'aki ne na tanti irin wanda Turawa ke yi bakin ruwa.

Cikinta ya duba ya ga babu komai ciki,hakan yasa ya gabatar masu da gasasar kaza wacce ta sha moutarde da yaji.
Kamar wadda ta shekara ba ci abinci ba haka ta ke yagar kazai shi kuma sai kallonta yake,yagowa ta yi ta kai bakin shi "ci!" ta fad'a ta na donawa a bakin shi murmushi yayi ya na mai bude baki ta tura mashi haka ta dinga bashi har ya 'koshi.

Ba ta wanke hannu ba balle brush kawai ta ganta tsaf kamar ba ta ci komai ba,hamma ta yi game da mi'ka ta na mai kallon tantin da ka na iya hangen shimfid'ar da ke ciki.Da kan shi ya kwantar da ita bisa lafiyayar matala ya na mai dadab'ata tare hura mata iska a fuska,wani wahaltacen barci ya d'auketa mai nauyi.

Cikin sauri William ya raba  su da jikinsu da kaya ya na mai hawa kan shimfid'ar,rungumota yayi ya sauke sanyayar ajiyar zuciya.
Mi'ka Maryam ta fara yi ta na fitar da numfashi tare da 'kan'kame jikinta,dundu Nadiya ta kai mata a baya "ke 'yar rainin hankali wai barci kike a shool koko dai munafurci ne dan mu ce baki lafiya shi yasa kika fito daga aji ba tare da kin bamu satar amsa ba?" Nadiya ke fad'in haka ta na mai girgiza Maryam wacce ke  kwance ,cikin jin haushi Karima tace "dan Allah 'kyale ta dan ta ga an damu da ita ne " daidai nan Maryam ta farka ta na mai jin kanta na sarawa da 'karfi,kai ta dafe ta na mai ambaton sunan Allah kafin ta fara kallon 'kawayen nata.

Cike da mamakin yadda idonta su ka yi ja har haka alhalin barcin bai wuce 30mns ba, "mi ya samu idon ki?ko wani abu ya fad'a maki?" Nadiya ta tambaye cike da tausayi,kai ta girta tace "wlh kaina ke min ciwo kamar zai fad'o" Maryam ta fad'a ta na shirin 'kara kwantawa Karima tace "tashi muje administration a baki magani daga can sai mu raka ki gida".

***

Cikin damuwa Laila ke kallon 'kawarta Zee kafin tace " wlh ina yi ma Nur son da uwa ke yi wa d'anta amman shi bai gani a kullum kushe 'ko'karina yake kawai dan nace babu tsarin rayuwar turawa a tsarina shine fa yake fushi da ni"tsuka Zee ta ja tace "ba doli ya dinga yawo da hankalin ki ba kin d'auki son duniya kin d'ora ma shi,kuma abun takaici sam baku dace da juna ba kamar yadda huta da ruwa ba sa iya zama wuri guda ba to haka misalin ku soyayyar ku yake.Kin ga ke ustaziya ce shi kuma d'an duniya ne so please kawai ki rabu da shi"

Kai Laila ta girgiza "ina son shi ta yaya zan iya rabuwa da shi? Sannan ki rin'ka gyara kallaman ki ,ki bar jifar shi da mumunar kalma"

"Miye na fad'a a nan?" cewar Zee
" d'an duniya fah kika ce kamar wani d'an ta'adda juste fah iyakar shi da 'yan mata romance ba wai wani abu can daban ba"

"Mtsw to tunda romance ba komi ba ne ki je kuyi kamar yadda ya bu'kata" Zee ta fad'a ta na mai mi'ke wa tsaye amman Laila ta ri'ke mata hannu,"haba 'kawata ina zaki kuma alhalin shawara nake so ki bani ?"a yadda tayi maganar sai ta ba Zee tausayi hakan yasa ta koma ta zauna tare da kamo hannuwan Laila "'kawata shawarar da zan baki kar ki tab'a bari gubar so ta rud'e ki ki je ki aikata abin da zaki zo ki na da na sani,dan haka kiyi taka tsantsa da Nur tunda kin ce ba ki iya rabuwa da shi kawai kice ma shi ya fito ku yi aure"

Cikin gamsuwa da shawar da 'kawarta ta bata ta jinjina kai tare da kunna data dan gaya mashi dan sun fi yin hira a wasap,texte ta rubuta masa na gaisuwa ganin ya na online sai dai maimakon ya amsa sai ya turo mata wata guntuwar vidéo play Zee ta danna nan suka ci karo da romance d'in da wasu suke yi sai fitar da numfashi su ke.

Wani irin zafi zuciyar Laila ta d'auka a lokacin da ta ga abun takaicin da ya turo mata,ta na shirin kashe data texte d'in shi ya shigo ````baby juste irin haka ne za muyi fa kuma ina mai tabbatar Miki ke ma  za ki ji dad'i sosai``` ta na karantawa hawaye su ka zubo mata na ba'kin ciki......

[14/10 à 07:29] MRS SADAUKI 💫: *MUTUM DA RIGAR ALJAN*👹

*Gajeren labari...*
Story
and
Written by
*MRS SADAUKI 💫✍*
{Cham rose💞}
Dedicated to *PRINCESS AYSHATOU*

☀ *FIRST CLASS WRITTERS ASSOCIATIONS*☀

---

BISMILLAHI RAHMANI RAHIM.

Page 18-19

A hanyar karb'o magani su ka gamu da Khalil,gaishe shi suka yi tare da fecewa suka bar Maryam ita d'aya.Cikin tausayi yake kallonta da idon shi da suka yi ja dan ciwo kafin yace "mine ne ke damun ki har haka ne?" langwab'ar da kai tayi tace "kasala ce kawai sai ciwon kai" "Allah sawa'ka jira ni a nan na yi déclaré sai na kai ki asibiti" ba ta ce komai ba har ya shiga ya fito.

A hanyar su ta komawa gida bayan sun je asibiti Khalil ya tsaya ya sayo mata fruits da jus,tun a hanya ta fara shan lemun dan wata irin yunwa take ji shi kuma sai kallon ta ya ke ta jikin madubin da ke a goshin mashin.

Ta madubin suka had'a ido tabbas Kalil ne ta fara ganin gabanin fuskar William ta bayyana d'auke da murmushi,mayar mashi ta yi ta na mai mashi fari da ido wanda ya zautar da Khalil dakyar dai suka isa gida lafiya.

Maryam na shiga room d'inta ta shige toilet dan yin fitsari,yadda  taji ne yasa abinda ya faru da ita ya dawo mata a kai,murmushi ta saki tace "je t'aime bien mon bb har sai yaushe zan gan ka a zahiri" ta 'karashe maganar da alamar tausayi a fuskarta.Wanka tayi tare da d'auro alwala sannan ta fito,riga marar nauyi ta saka ta na mai d'aukar al'kur'ani mai girma cikin sanyayar muryata ta fara kwararo 'kira wacce ta ke ba ko wane harafi ha'kin shi,hawaye ne suka fara kwaranyo mata lokacin da ta zo daidai ayar يمعشر ٱ *لجن* وٱلإنس إن ستطعتم ان تنفذ ومن أقطار ٱاسموت و

ٱلأرض فٱنفذو لا تنفذون الا بسلطن rufe 'kur'anin tayi wanda ba ta san dalilin 'kin jin dad'in ba kalma guda ta ke furtawa *JINN*  kamin tace "su ma har da su kenan?tare da mu za'a had'e su ayi mana hisabi duka kuma zamu tsaya a gaban Allah mad'aukakin sarki gagara misali amman kam ni ba zan jurar kallon aljanu ba" ta fad'a da alamun tsoro fuskarta a take kuma tsohuwar da ta ke yawan gani a mafarki ta shiga yi mata gizo 'kan'kame jikinta ta yi ta na mai karanto duk addu'ar da ta zo bakin ta.

A b'angaren Khalil kuwa ko da ya shiga part d'in shi kan bed ya fad'a tare da rufe ido ya na murmushi tare da tunano yadda Maryam take faman 'kan'kame shi ba ta son allura,taushin jikinta shi ya fi komi tafiya da hankalin shi.Tsikar jikin shi ce ta shiga tashi yayin da wani abu ya fara lulub'e shi,saurin kawar da tunanin yayi ta hanyar tashi yayi wanka ya fito waje ya d'ora shayi.

***

Abu kamar da wasa Laila ta tsiri fushi da Nur duka number shi tayi blocking sai dai ruhinta ya kasa samun nutsuwa hakan yasa ta bud'e, ko mintin 5 ba ayi ba kiran shi ya shigo.'Dagawa ta yi ba tare da tace komai ba,ajiyar heart ya sauke ya na mai jin wani sanyi na ratsa shi dan bai yarda ya na son Laila ba har haka sai lokacin da ta li'ke duk hanyar da za ta sada su.

"Assalamu aleyki" cewar Nur,lumshe ido ta yi ta na jin dad'i karo na farko kenan da ta fara jin Nur yayi mata sallama.Amsawa ta yi nan ya fara bata ha'kuri tare da nuna mata babbar illa da zai samu in ta yi banzatar da shi,sosai Nur ya za'ke ya na kwararo mata kallaman soyayya masu tsayawa a rai a 'karshe yayi mata al'kawarin aure tare da turo mata number mahaifiyar shi.

Tsalle da rawa Laila ta shiga yi dan murna a take ta shaidawa Zee,kafin tayi sujadda shukur.

A b'angaren Nur kuwa sosai ya ke jin hutar son Laila na huruwa a ran shi,dan har ji ya ke kamar ita ce numfashin shi.
Da farko ya so yin watsi da Elli sai dai kuma yanayin yadda ya ke jin feeling yasa shi 'kin rabuwa da ita.....
[14/10 à 07:43] MRS SADAUKI 💫: *MUTUM DA RIGAR ALJAN*👹

*Gajeren labari...*

Story
and
Written by
*MRS SADAUKI*
{Cham rose💞}
Dedicated to *PRINCESS AYSHATOU*

☀️ *FIRST CLASS WRITTERS ASSOCIATIONS*☀️

BISMILLAHI RAHMANI RAHIM.

Page 20-21

A tsanake ta ke shiryawa sai murmushi take zubawa tamkar wacce aka yi ma bushara da gidan aljanna,yau shiga fararen kaya ta yi tun daga hijab,takalmi da kuma bag.Umma ta yi ma sallama ta na mai wucewa school,tun daga nesa ta tsinkayi Nur a bakin 'kofa ya had'e cikin riga da wando na shadda kamar wani mutumen 'kwarai.

Duk da fuskarta a rufe take da ni'kaf sai da 'kirjin shi ya buga,ganin irin surar da ya fi so a rayuwa shap coca cola.A hankali take tafiya ta na rangaji kamar hanwainiya duk tako d'aya sai jikinta ya motsa.Yawu Nur ya had'iye ya na mai yin tasbihi ga Allah,direct inda ya ke a tsaye ta nufo ta na kawowa gaf da shi tayi mashi sallama cikin cool voice murmushi mai sauti yayi kafin ya amsa.

Shiru wurin ya d'auka sai wasa take da zoben hannunta yayinda shi kuma ya ke 'kare mata kallo,wuci mai zafi Nur ya sauke ya na mai cewa "baby yanzu rowar kyakyawar fuskar taki zaki yi min?ko baki ji dadin ganina ba ne na koma?" da sauri ta d'ako kai caraf idon su ya shiga juna,girgiza kai tayi ta na mai d'age ni'kaf d'in sama "masha Allah babyna haka kike da kyau?Allah ba ni ikon mallakar ki" da "amen" ta amsa ta na mai sakin murmushi wanda yasa dimple d'in ta lotsawa.

Agogon hannun shi ya duba kafin yace "zan wuce in kun tashi ki yi min signe" kai kawai ta jinjina ta na jin sam babu dad'i zai tafi ya barta duk da su na da cours.

Turus tayi ganin Zee tsaye ta na kallon su "wai dama ke ce ?wanene wancan d'in?"Zee ta

tambaya ta na girgiza 'kugu,dariya Laila tayi ta ce " Nur mana ko baki gane shi ba?"cike da mamaki Zee tace "au!salon yaudarar da ya d'auko kenan?" b'ata fuska Laila ta yi ta ce "miye na yaudara kuma?"
"Dogayen kaya da ya saka har da wata hullar sharri hum!to tsaya ki ji yarinya kar ki yi saurin yarda da shi don namiji d'an maciji ne" cikin b'acin rai Laila ta d'aga ma Zee hannu"ya ishe ki haka babu ruwan ki da rayuwata,kenan ke duk abinda Nur zai yi sai kin fassara shi to miye laifin shigar shi 'kila kawai dan yaji nace suna burge ni ne"ita ma Zee cikin jin haushi tace "ke malama ki shiga taitayin ki wlh namiji ba dan goyo ba ne yadda kika san balbela haka ya ke amman ba komi je ki jiki magayi" fuuu Zee ta wuce ta bar Laila tsaye.

A b'angaren Nur kuwa ya na zuwa room d'in shi ya cire kayan dan ji ya yi sun dame shi tamkar ya saka rigar 'kaya, cikin 'kananun kaya ya shirya ya na mai d'auko carte d'in da Elli ta ba shi jiya na gayyata.

Adresse d'in gidan da ta d'auka haya ne dan cikin school jin ta take a takure,babu wani nisa da école hakan yasa Nur saurin kaiwa.
Ihu Elli ta yi ta na mai fad'awa cikin jikin shi tare da kai mashi kiss ta ko ina "na zata ba zaka zo ba ganin har takwas ta gota"cewar Elli ta na mai jawo hannun shi izuwa cikin d'aki.

A salon suka baje suka fara ciye-ciye tare da masha'a,yau salon da Nur ya ke tafiyar da Elli na daban ne domin ya lashi takobin sai ya ratsata.Da salon shi na mayaudara har yayi nasarar raba su da kayan jikin su,duk da yau ne karo na farko da zai fara kusantar mace bai sa shi jin tsoro ko wani d'ar ba.

Babu zato balle tsammani Elli ta ji wani azababen zafi na ratsa 'kasanta,ihu ta 'kwala tare da suratai irin na hausar garin su " oh mon Dieu Nur mi kike mani tu cesse j n veux pas zafi,zafi nik...."saurin game bakin su yayi ya ci gaba da azabtar da ita wanda ya ke ji wani yanayi na daban na shigar shi.

Bai wani dad'e ba ya rabu da ita,rarashin ta ya shiga yi inda ya ke ce mata "bb calme toi !de toutes les façons ni zan auren ki to miye kuma na kuka" duk da Elli na cikin mawuyacin hali bai hanata jin dad'i ba jin zai aure ta.

***

"Mother ki fahimce ni mana ina son tafiya duniyar bil'adama dan cika burin mu wanda muka dad'e muna tsarawa" cewar William ya na mai sake matsowa kusa da mahaifiyar tashi wacce ta bashi baya tun lokacin da ya zo mata da maganar.

"Wannan ba shi cikin tsarina d'aukar fansa shine burina ba wai ka so Maryam ba,na barka ka na kasancewa da ita ne dan cutar da rayuwarta ba wai ka aure ta ba" mother ta fad'a cikin muryarta wadda ba ta da dad'in amo,kusa da ita ya 'kara matsowa yace "na kasance mai maki biyayya mother duk da har yanzu ban san dalilin ki na son d'aukar fansa ba amman dai na san kawai kin tsani Maryam wanda ni kuma sam hakan bai min dad'i ba"wata irin dariya mother ta shiga 'kyar'kyatawa kafin ta tsagaita " tabbas ina son ganin farin ciki ya gushewa wannan ahalin,zab'i biyu zan baka doli ka d'au d'aya na farko zan haukata Maryam daga 'karshe na kasheta na biyu kuma sai in dai zaka samar min jika wanda cikin zai fito har kowa ya san da shi wannan sune sharad'a na"cewar mother ta na mai kartar fuskarta da zara-zaran akaifun yatsunta kafin ta b'ace b'at ta bar William cikin zullumi wane zab'i zai d'auka na d'aya ko na biyu......
[16/10 à 10:04] MRS SADAUKI 💫: *MUTUM DA RIGAR ALJAN*👹

*Gajeren labari...*
Story
and
Written by
*MRS SADAUKI 💫✍️*
{Cham rose💞}
Dedicated to *PRINCESS AYSHATOU*

☀️ *FIRST CLASS WRITTERS ASSOCIATIONS*☀️

---

BISMILLAHI RAHMANI RAHIM.

Page 22-23

Wanka suka shiga tamkar wasu ma'aurata,sosai Nur ya gasa Elli ita kuma sai shagwab'e mashi take.
Bayan sun shirya suka koma cin abinci kafin barcin wahala ya d'auke Elli shi kuma Nur ya danna ma Laila kira.

"Assalamu aleyka yaa zauji" cewar Laila tare da yin murmushi mai sauti,lumshe ido yayi ya na jin wata nutsuwa na sauko mashi kafin ya amsa da "wa'aleyki salam sahibata da fatan kin yi cours cikin 'koshi lafiya?"
"Um komai daidai ,sai kewar ka da na yi" ta faɗa cikin murya tausayi,y'ar dariya yayi kafin yace "baby ni ma fah na yi kewar ki ji nake kamar na ganki gabana na rungume ki" b'ata fuska Laila ta yi kamar ya na ganinta tace "kenan dai?"
"Eh mana ko baki so ne?"
"Wai ka na ina ne?" Laila ta fad'i haka dan son b'atar da zancen ,gashin Elli ya shafa kafin yace "ina gida mana ya aka yi ne?"d'an jimmm ta yi sai kuma tace "yau ba ka fita ne?ko yau babu football d'in?"
"Akwai ba dai zan samun damar zuwa ba ne" cike da mamaki Laila tace "wane abu ne mai mahimmanci har zai hana ka zuwa 'kwallo?"inda-inda Nur ya fara abun ka da wanda bai saba 'karya ba sai fad'in gaskiya komin d'acinta hakan yasa Laila saurin d'ago shi " kar ka min 'karya faɗa min gaskiya" a yadda ta yi maganar a dake yasa 'kirjin Nur dukan uku-uku cikin 'karfin hali ya ce "bari za mu yi magana an jima yanzu..." saurin katse shi ta yi da cewa "ni yanzu nake so babu wani sai an jima kuma billahil azim kar ka min 'karya dan da ka yi sai na gane".

Cikin sanyin murya Nur yace " to ki yi min al'kawali ba za ki ji haushi ba sannan ba za ki d'aukar tsatsauraran mataki ba?"
"In shaa Allah muddin ka fada min gaskiya"
"Hummm babyna ita rayuwa ta na zuwar ma bawa ne a yanayin yadda Allah ya tsara wa ɗan Adam ita,sannan duk dabarar mutum bai isa ya guje ma kaddarar shi ba" ɗan tsaya wa yayi yayin da ita kuma jikinta yayi sanyi tace "haka ne ha'ki'ka babu wata fitina ko akasin haka da zai samu bawa fa ce al'kaluman shi sun rigayi hakan amman miye ke damunka?"

"Am!Laila tun can farko Allah ya jarabce ni da ciwon sha'awa tun ina d'an 'karamina,na san ke ma kin lura da haka ?" cikin sanyin murya Laila tace "eh kusan haka ne mine ne ya same ka?" tayi tambayar cikin 'kaguwa.

"Kin san yadda ƴan matan school d'in nan su ke kawo min hari ko?to a haka har suka shawo kaina na fara rayuwa turawa to shine kuma yau,yau kuma sai..." kasa idawa yayi saboda yadda zuciyar shi ta karaya da kuma jin nauyin maganar .

"Shi ne mi kuma me Nur?kar kace min ka kusanci mace please no ba zan juri haka ba kar ka ce min haka kai nawa ne ni kaɗai,dan Allah faɗa min mi ya faru?"ta 'karashe maganar zuciyarta na karye wa yayin da muryarta ta shiga karkarwa,cike da tausayinta yace " ki yi shiru please wlh ni ma ba da son raina hakan ta faru ba"Nur ya fad'a cikin nadama,wani irin gumi ne ya shika

tsatsab'o ma Laila kafin wani sanyi ya mamaye jikinta....

***

Zaune yake cikin damuwa ya rasa mi ke ma shi dadi,mother na fushi da shi sam duniyar babu dad'i.
Motsin da ya ji ne yasa shi d'agowa, a tsaye take ta bashi baya kamar ko da yaushe,cikin raunananar murya yace "mother ?" 'kin amsawa ta yi sai wani huci da ta fara fitarwa kamar kumurcin zaki zuwa can ta juyo tare da yarwa hannunta saitin William a take ya saki 'kara ya na mai shemewa.

Wata irin dariya mother ta fara yi tare da magana cikin muryarta marar dad'in amo "daukar fansa shine burin duk wani *JINN* da aka cutar ba tausayi ko soyayya ba dan haka na d'aure ka zaka zauna a nan har sai na kammala aikina"

'Dago idanu William yayi uwanda suka fara lumshe masa kamar irin na wanda zai bar duniya,kai kawai ya shiga girgiza ma mother alamun kar ta aiwatar da 'kudirin ta.......
[16/10 à 10:14] MRS SADAUKI 💫: *MUTUM DA RIGAR ALJAN*👹

*Gajeren labari...*
Story
 and
  Written by
*MRS SADAUKI💫✍🏻*
 {Cham rose💞}
Dedicated to *PRINCESS AYSHATOU*

☀️ *FIRST CLASS WRITTERS ASSOCIATIONS*☀️

BISMILLAHI RAHMANI RAHIM.

Page 24-25

Cike da zullumi Maryam ta rakub'e wuri guda,correction d'in interrogation ake amman sam hankalinta bai wajen mushen har ya fara bada copie.

Duk ajin babu wanda ya samu 6/20 sai Maryam da ta samu 20/20,tab'in da taji ana yi ne ya maidota daga duniyar tunanin da take.Nadiya ce ta dan zungureta ta yi mata alama da ta tafi ta karb'o sakamako amman abun mamaki kasa tashi ta yi har table d'in Mr Marwan ya kawo mata copie tare da jifar ta da wani mayen kallo wanda ya 'kara sakar ma Maryam wata kasala,saurin lumshe ido ta yi zuciyarta na bugawa.

Duk idanun students ne ya dawo kan su ganin Mr Marwan ya rankwab'o ya na yi ma Maryam rad'a a kunne,"mi ke damun ki beauty?ko baki ga ke ce kawai kika lashe jarabawar please ki tashi"Mr Marwan ke fad'a daidai saitin kunnenta,wani iri ta ji a jikinta ba tare da ta san maganar ta fito bakinta ba tace "banda lafiya"
"Mike damun ki?to tashi ki karb'o magani " ya na gama fad'in haka ya ce ma su Nadiya su fita da ita.

Lokacin cours d'in shi bai 'kare ba ya fito cikin sauri ya cimma su Karima,umarni ya basu su shiga motar shi dan kaita asibiti.Dukan su baya suka shiga Maryam na zaune a tsakiyar su,Mr Marwan na driving amman hankalin shi na kanta a haka har suka kawo asibiti.

Abun mamaki gwajin duniya amman ba a ga komai ba,cikin sanyin murya tace "ni fah lafiyata lau kawai kasala ce nake ji" jin haka yasa aka bata magani suka dawo school.

"Ni kam sai nake gani kamar Mr na son Maryam ko baki lura da haka ba ne Nadiya?" maimakon ta bata amsa sai cewa tayi "ni fah abin da ya d'aure min kai tayaya kika canye jarabawa alhalin wani cours ba muyi shi ba ma?" murmushi Maryam tayi jin an tab'o inda ya ke mata 'kyai'kai "shi ya fada min fa ko baku lura ba lokacin..." wani irin sarawa da kanta yayi ne ya hanata 'karasawa sai gani suka yi ta dafe kai.

Mother POV.

Tun lokacin da ta kwantar da William ta fito ta shiga shawagi a duniyar bil'adam,sosai ta ci wuya

wajen samun galaba gun Maryam.
Tun su na mota ita da Khalil ta so ta had'a masu hatsari sai dai 'kira'ar da ke tashi a mota ya hanata samun nasara,a lokacin da Maryam zata fitowa a mota da sadda ta shiga classe duk sai da ta yi bisimila hakan yasa mother ta zauna bisa wata bishiyar mangoro.

Mr Marwan na sauke su a mota suka nufi bishiyar mangoro babu wani neman tsari suka baje suka fara labarai a daidai nan mother ta yi tsalle ta shige cikin kan Maryam.

Da sauri Karima ta ri'keta yayin da Nadiya ta kirawo Kvalil,yanayin yadda idon Maryam suka kafe ba 'karamin girgiza su yayi ba dakyal suka kaita mota cikin kuka.

Tamkar wata matatta haka ta sheme cikin mota babu inda yake motsawa a jikinta sai ido da suke fama juyawa kamar 'yar tsana,dardumar da ke shimfid'e a cikin rumfa suka ajiyeta tare da taimakon Khalil.

Khalil na tsaka da yin ru'kiya cikin ruwa umma ta fito daga d'aki,ba ta tsaya tambayar lafiya ba ganin yadda 'kawayen Maryam ke zaune kusa da ita suna kuka yayinda Kvalil ke ta tofi a kofi.

Wata irin juwa ce ta d'ebi umma da sauri ta zauna sharaf a kujera ta na maida numfashi,ihun Maryam ne ya sa ta dawowa daga sumen wucen gadin da ta yi.

"Ku ri'ke min ita da 'karfi" cewar Khalil ya na mai tab'e bakinta ya kwarara mata ruwan addu'ar sauran kuma ya zuba mata a kai,wani gurnani ta fara tare da she'kewa da dariya tace "umma munafuka maciyiyar amana mi kika zo yi nan?hhhh wai umma yaushe kika fara jin tausayi dan Adam ?" dukan su kallonta suke cike da mamaki ba ma kamar umma jin munanan kalamman da 'yarta take jifar ta da shi kafin su shanye mamaki sai ganin Maryam suka yi ta bingire barci.

****

Wani irin so da tausayin Nur ke addabar zuciyar Laila,tabbas son gaskiya daban yake domin in

ba haka ba da tuni ta bar Nur sai dai zuciyarta ba zata iya jurar haka ba.Addu'a da neman shiriya take ma shi a cewarta 'kaddarar shi ce wannan haka Allah ya tsara ma shi rayuwa.

A b'angaren Nur kuwa wata irin kunyar Laila ya ke ji a d'aya b'angaren kuma sosai suke she'ke ayar su shi da Elli abun kuma takaici duk in yayi sai ya ba Laila labari wanda hakan na faruwa ne sakamakon yawan tambayoyin da take masa.

Yau da gobe ba ta bar komai ba Nur ya fara cin galaba gun Laila,dan yanzu sosai ta ke tsayawa ta na sauraren hirar shi wadda ba ta da wani amfani face sai b'ata da rabkanuwa cikin sab'on Allah.

Kwance take bisa gado ta lumshe ido ta na lisafo siffar Nur irin yadda ta ganshi babu riga 'kasumba cike da fafad'an 'kirjin shi ga sajen shi wanda ya f komai burge ta a tatare da shi.

"Zan so na kasance da kai,na kwanta kan ƙirjinka" ta fad'i haka ta na murmurshi......
[16/10 à 10:34] MRS SADAUKI 💫: *MUTUM DA RIGAR ALJAN*👹

*Gajeren labari...*
Story
and
Written by
*MRS SADAUKI💫✍🏻*
{Cham rose💞}
Dedicated to *PRINCESS AYSHATOU*

☀️ *FIRST CLASS WRITTERS ASSOCIATIONS*☀️

BISMILLAHI RAHMANI RAHIM.

Alherin Allah ya kaima duk wani wanda ke son ki habibaty *mss flower*🌸 son so fisabilillah❤️

Page 26-27

Sosai hankalin Laila ya tashi saboda d'an tunanin da tayi akan Nur,jikinta duk ya saki.

Cikin kewarsata danna masa kira buga d'aya ya ɗauka, numfashi ta sauke tare da rufe ido ta na sauraren kirarin da Nur ke jero mata "amincin Allah ya tabbata ga sarauniyar kyau,mai hasken taurari,ma'abociyar fara'a,mai kyawun fasali da 'kayatacen dimple mai bayyanar da wushiryar fararen ha'korinta" d'an jan fasali yayi game da numfashi kafin ya d'ora da "fatan ki na lafiya dai?" sai da ta 'kara rumtse idonta saboda salon yadda yayi maganar.Dakyar ta iya furta"eh lafiya lau nake!" d'an jim yayi kafin yace "mi ya samu muryar ki na ji ta haka?Ko ba ki lafiya?" kai ta girgiza kamar ya na ganinta kafin tayi 'karfin halin cewa "kawai ina jin kasala sinon je me porte bien" murmushi yayi nasu na yan duniya yace "mi ya kawo kasalar?Ko sabuwar fura kika sha?" "a'a" ta bashi amsa.

Huging nashi Iki ta yi kasancewar a tsaye ya ke cikin filin da aka tanada dan sha'katawa,kafin Nur yayi wani yun'kuri har Iki ta kewayo ta gaban shi ta na facing na shi.
Kashe kiran yayi ya maida wayar a aljihu cike da masifa ya nuna Ikilima sai dai ko kalma d'aya ba ta bari ya furta ba ta game bakin su,a yadda take kissing kad'ai ya isa ya tabbatar da Iki ta dad'e cikin yan duniya saboda lokaci guda ta rikita shi.

Bayan wata rumfa ya jata nan suka ci gaba da masha'ar su har Nur yayi nasara cin galaba akan Ikilima,wata irin azaba taji ta ratsata .Kuka ta shiga yi wa Nur ta na zaginsa.

A can ɓangaren Laila kuwa sosai ta ji haushin yadda Nur ya yi mata.
Wani wahaltacen barci yayi awon gaba da ita bayan dogon lokacin da ta d'auka ta na jiran ko Nur ya maido kira.

Wasu manya 'beraye ne masu kama da gayya ke cin naman farjinta yayinda jini sai ambaliya yake,ita kuma sai kuka take ta na neman taimako amman shiru kake ji.Sosai take 'ko'karin janye b'erar amman ta kasa sai ma 'kara hudata da yake,ta na gab da farkawa taji wata murya na ce mata "wannan shine hukunci mazinaciya",firgigit Laila ta farka cike da tsoro ta na dafe 'kirji.

***

Sosai take gudun ceton rai babu 'ka'kautawa,cikin jikinta shi ke tsayar da ita dan sosai ta gaji. Ta na shirin zaunawa sai ji tayi 'kasa na rumzawa da ita,can ta fad'o cikin wani rame mai cike da 'karangiya daidai nan d'an cikinta ya fad'o tare da canyara 'kara.
Wani hannu mai d'auke da zara-zaran yan yatsu da manya akaifu ya cabki jinjirin kafin mamalakiya hannun fuskarta ta bayyana.

Kamar cikin barci ta ji a na tashin ta,ido ta bud'e ta na mai dafe kanta da take jin yayi mata nauyi.
Mafarkin da tayi ya dawo mata a kai a take fuskarta ta nuna alamun tsoro," Maryam ya jikin naki"cewar Khalil ya na kallon face na ta.

Samun kanta ta yi da yi masa murmushi wanda yayi mugun tafiya da hankalin Kvalil,cike da jin dad'i yace "ya jikin naki?"
"Da sau'ki yunwa nake ji" Maryam ta bashi amsa "OK bari na je na nemo maki kinji babyna?" d'aga kai ta yi tare da tashi ta nufi toilet dan kurkuro baki.

Shinkafa fara ce wadda ta sha man gyad'a da zogale,da kan shi yake bata a baki har ta 'koshi. Ruwa masu sanfi ya bata ta sha kafin yace "tashi ki yi sallah"fara'ar fuskarta ce ta d'auke yayinda ta ji wani ba'kin ciki ya ziyarci zuciyarta,cikin shagwab'ar da ita kanta ba ta san da ita ba ta fad'a 'kirjin Kvalil tace " ni kwana nake ji na gaji wlh"wani shau'ki ya d'ibi Khalil nan ya shiga bubuga bayanta ita kuma ta lafe kamar wata mage.

Barci mai cike da rud'ani da firgici ne ya d'auke Mayam,wanda ita kad'ai ta san munanan abubuwan da take gani tare da azabar da take sha.

A b'angare guda kuma Khalil ne gefenta ya 'kura mata ido ya na yaba kyawun surar jikinta tare da ayyane wasu buruka game da ita.
Ajiyar zuciya ya sauke mai 'karfi ya na jin wani sabon sonta,'kaunarta da sha'awarta na tsarga mashi.Fuskarta ya shafa da bayan hannun kamin ya furta "i love you" abun mamaki sai ya ga tayi murmushi hakan ba 'karamin dad'i yayi ma shi yasa ya ci gaba da cewa "baby baki yi bacci ba kenan?kin san yadda nake son ki kuwa?tamkar yadda uwa ke son d'anta ko kuma nace fiye ma dan...." shigowar momy ce ta katse shi wadda ta ji sarai abin da yake furtawa.

"Ai shikenan ka ga ana basu hutun school sai ayi bikin ku kuje can ku 'karata" cewar momy ta na mai mi'ka ma Kalil kofin shayi, 'keya ya d'an sosa alamun jin kunya "momy Allah sa babyn ta amince" "na amince" shine abin da Maryam ta faɗa murmushi a kan fuskarta ta na mai gyara kwanci.

"To ba ka ji ba dama auren take so shiyasa ta fara raina ni har take neman fin 'karfina ta na

mayar min da magana sai kace ita ta haife ni" momy ta fada ta na hararen Maryam.

Dariya Kvalil yayi ya na mai mi'kewa "momy ba hakanan ba ne kawai  'kurciya ce ke damunta amman nan da d'an lokaci ta daina" ko kinzil momy ba ta ce ba ta samu wuri ta zauna yayinda shi kuma ya fice.

Fitar Khalil ke da wuya fuskar Maryam ta rikid'a ta zama ta wata mata wace ba zata wuce 30years ba,'kuri momy ta sake yi ma Maryam dan tabbatar da abin da idonta ke mata gizau fuskar nan dai ta sake gani ba ta Maryam ba.

'Kirji ta dafe  "na shiga uku ni Talatu mi nake gani kuma kamar fuskar Suweiba"ta fad'i haka ta na shirin juyawa ta bar d'akin kawai sai ta ga 'kofa ta rufe da kanta ta sa key yayin da makulin ya fara nufota a hankali ita kuma ta na yin baya-baya har ta kai jikin gado.

Tsalle ta yi ta bi ta jikin Maryam sai jin wata murwa wacce ba za ta tab'a mantawa ba ta na ce mata " Talatu d'aga ni kar ki kashe ni"ihu momy ta runtuma tare da zubewa sumamiya.

Awa wajen uku kenan a na abu guda faman 'kara ma momy ruwa amman har yanzu ba ta farfad'o ba,sai ma wani jijiga da take alamun furgici likitoci kuma sai faman scaning suke na 'kwa'kwalwa yayin da gefe guda kuma Maryam sai rizgar kuka take ta na faman kiran momy abin da kuma suka kasa fahimta duk lokacin da Maryam ta ambaceta to murya Suweiba momy ke ji  wanda hakan ke sa ta jijiga.

Wani likita ne da ya lura da haka yace Khalil ya fitar da Maryam,hakan kuwa aka yi can wajen asibitin suka fito ya na bata ha'kuri da rarrashinta.

Su na fita momy ta farka sai faman ajiyar zuciya take,"sannu madame "cewar nurse " yauwa dan Allah kar ku bari wannan macen ta sake shigowa ban son ganinta"momy ta fad'a ta na kuka.
Cike da mamaki nurse d'in tace "wace mace ko wannan yarinyar?" kai momy ta d'aga mata ta na share zufar da ke keto mata.Kallon Dr nurse ta yi wanda yayi sa'ke ya na nazarin momy.

***

Jiki babu 'kwari Laila ta yi wanka tare da sallah kafin ta d'auki al'kur'ani ta karanta wanda sam babu nutsuwa domin mafarkin da tayi sai yawo ya ke mata a cikin kwanya.
Zuciyarta a cunkushe ta fito dan d'ora girkin marice, ba ta tarar da kowa ba hakan yasa ta shige madafa ta fara girka tuwon shinkafa da miyar kub'ewa d'anya.

Siraci ne ya bugi hannunta a take ta 'kwala 'kara sai kuma tayi sa'ke ta na maganar zuci "toh ina ga hutar jahannama?wlh na tsani kaina ma tunda har na fara tunanin aikata sab'on Allah mafi muni wai Zina kaiiii amman Laila kinji haushi" duk a zuci take maganar,hawayen da suka kwaranyo mata ta goge kamin ta ci-gaba da aikin da take.

A b'angaren Nur kuwa wani irin tausayin Iki yaji na rabata da Virgin nata yayinda kuma b'angare d'aya na zuciyar shi ya ke jin damshin sonta.Ita kuma baiwar Allah sai bayan sun tabka kuskure ta shiga nadama tare da fargaba kar Nur yace bai auren ta.......
[18/10 à 11:08] MRS SADAUKI 💫: *MUTUM DA RIGAR ALJAN*👹

*Gajeren labari...*
Story
and
Written by
*MRS SADAUKI💫✍🏻*
{Cham rose💞}
Dedicated to *PRINCESS AYSHATOU*

☀️ *FIRST CLASS WRITTERS ASSOCIATIONS*☀️

---

BISMILLAHI RAHMANI RAHIM.

Page 28-29

Kwance take ta lumshe ido sai saƙa da warwara take,ta rasa abin da ke mata daɗi komai ya jagule mata dan ko abinci ta kasa ci.Ba wani abu ba ne ke damunta face halin ko in kula da Nur yake mata tun ranar da suka yi wayar ƙarshe inda har ta so tabi son zuciya ta faɗa kogin nadama sai kuma mafarkin da tayi ya taka mata burki.

Ƙara jaraba kiran lambar Nur ta yi a karo na barkatai amman shiru har ta yanke bai ɗaga ba,wasu siraren hawaye ne suka shiga kwaranyo mata ta gefen ido suna jiƙa pilown da ta ɗora kanta.

Ba ta taɓa sanin ta na son Nur ba sai yanzu da ya ƙaurace mata wanda ba ta san dalilin yin haka ba,hannu ta ji a fuskarta ana goge mata hawaye ba ta buɗe ido ba sai tsinkayo murya Rahila ta yi tana cewa "kiyi haƙuri anty ki bar kuka ki maida lamarin ki da Allah,kar fah ki manta a ko da yaushe umma na tunatar da mu da cewa duk wanda ya baiwa Allah ragamar rayuwar shi to ba zai taɓa ƙasƙanta ba"Rahila ta ƙarashe maganar cikin raunananiyar murya.

Murmushi mai ɗauke da hawaye Laila ta yi tana mai tashi zaune ta rungume ƙanwarta,cikin murya kuka tace "na gode sosai da tunatarwa my ƙanwa haƙiƙa na kasance mai sa'ar kasancewar samun ki a matsayin ƴar uwa"ta faɗi hakan tana mai jan ajiyar zuciya tare da huci mai ƙarfi kafin ta kuma cewa "ya kin ci abinci?"kai Rahila ta girgiza "ke na ke jira ai tun ɗazu nake jiran fitowar ki amman ba ki fito ba shine na zo kiran ki kar tuwon ya huce"cewar Rahila tana mai miƙewa tsaye "ok tafi ki jira ni".

Sai da ta goge fuskarta da kyau ta yadda umma ba za ta gane tayi kuka ba kafin ta fita,bisa tabarma ta zauna kusa da Rahila wacce tun tuni ta sa kwanon tuwo gaba tana jiranta.

Abincin suka fara ci wanda rabin hankalin su ya na kan tv inda ake haska wani série TÉRÉSA,cak Laila ta tsaya da barin cin tuwon lokacin da aka buɗo jarumin film ɗin yana kissing budurwa shi tare da jifarta da kalaman soyayya.

Rumtse ido ta yi tana ji tsikar jikinta na tashi yayin da kwanyarta ke hasaso mata yadda abun zai kasance ita da Nur.

Tsawar da Abba ya daka mata ne yayi sanadiyar ɗaukewar uban murmushin da take zubawa tare da maidota daga duniyar tunanin da ta lula.

"Sannu da zuwa Abba "ta faɗa cikin rawar murya,bai amsa ba sai wani kallon tsaf da ya ke bin ta shi kafin ya wuce inda umma ke zaune wadda gama sallah ta kenan.Ledar hannun shi ya ajiye kafin yace "uwar yara yanzu ban hana ki saka tashar turawa a gidan nan ba?shine kika wani zo ki na jan cazbaha su kuma suna kallon tv duk abin da za su kalla ke ba ruwan ki"sunkuyar da kai umma ta yi kafin ta shiga bashi haƙuri maimakon ya sauka sai kuma ya sake hawa "wane haƙuri zaki bani bayan ki na son gurɓata tarbiyyar yarana?yanzu sabida Allah hakan ya dace ke kina aikin Allah su kuma ko sallah ba su yi ba amman ke hankalin ki kwance? Abba ya tambaya cikin ɗaga murya wanda yasa ran umma ɓaci "haba mai gida su wasu ƙananun yara ne da basu san daidai ba da kullum sai nace suyi sallah?"cewar umma ta na mai ninke tapis.

Sasauta murya Abba yayi yace "amman kin san saboda su muna iya shiga wuta ko?domin Allah yace mu kula da kan mu da ƴaƴan mu daga shiga huta,yanzu za ki ji daɗi ki na aljanna yaran ki na wuta?"cikin rashin jin daɗin yadda umma ta mayar mashi da magana tace "kayi haƙuri tabbas ba zan ji daɗi ba kuma na sani ƴaƴanmu kiyo ne a gare mu kuma ranar lahira sai Allah yayi mana bincike akan irin yadda muka kiyaya su"murmushi Abba yayi najin daɗin kallamanta dan tabbas shi da kan shi yasan umma ta na cikin nagartatun mata domin tun can saboda addinin ta ya aure ta.

"Alhamdullah tunda kin fahimta yanzu sai a kiyaye bance kar a kalli tv amman a san abin da za ayi kallo,ku kuma maza ku tashi ku yi sallah"cewar Abba ya na mai shiga ɗakin shi.

NUR POV.

Tun lokacin da ya ɓare Ikilima cikin ledarta ya rasa sukuni,sam bai ji ya na maradin komai kamar ya kasance da ita sosai Elli ta ga canji ta yadda ya ke wani shareta dakyal take samun shi shi ma ba wani jamawa yake ba gidanta in ma yaje bai wuce romance.

Tun Elli ba ta damuwa har takai ta kasa ɓoyewa ta sanar da Esta nan ne Esta take ce mata "ai kin makkaro domin yanzu ya samu sabuwa a leda ya bar yayin ki"kallon ban gane ba Elli tayi mata ita kuma ta cigaba da cewa "eh mana ko baki san sun jone shi da Iki ba?ai tuni ya garwaya da ita kuma shine first da ya fara saninta a ƴa mace" ƙwallo ido Elli tayi tace "na shiga uku wai da gaske kike ko wasa?ita Ikin ta faɗa maki haka?"dariya Esta tayi tace "babu wanda ya gaya mani ni na sani da kaina kuma na gaya maki ne dan ki fidda rai"rufe bakin Esta ke da wuya Elli ta fara kuka tana suratai tare da zayyano irin moments ɗin da suka yi masu daɗi

wanda har ya kai yasa zuciyar Esta ayyana wani ƙudiri.

Tun bayan magrib gaban Nur ke faɗuwa haka kawai ya ji ra'ayin karanta alƙur'ani mai girma,cike da nutsuwa yake karatun cikin sauti mai daɗi ya ɗauki lokaci kafin ya tashi ya tafi masallaci yana dawowa kuma ya ci gaba.
Sosai ya ji zuciyar shi ta yi sanyi tare da samun nutsuwa,rabon da yayi karatun al'ƙur'ani har ya manta sai yau kuma ba dan bai iya ba.

Sai da yayi addu'a sosai kafin ya maida ƙur'anin,sai a lokacin Rahul ya shigo ɗakin ya na ƙanƙame jiki kamar mai jin sanyi.

Ɗan buɗe ido Nur yayi ya kalle shi kafin ya taɓe baki yace "an dawo daga yawon shaƙatawar?"ya faɗi hakan yana mai yi wa Rahul kallon tsaf,harara ya zabga mashi ce "dalla can malam wane yawon shaƙatawa bayan duk ka wani takura ni da karatun ka"cewar Rahul ya na mai hayewa kan bed,tashi zaune Nur yayi cike da mamaki yace "yanzu ƙiyayar musulunci har ta kai haka ga zuciyar ka ta yadda har karatun al'ƙur'ani zai takura ka?shi fah waraka ne ga al'umma"martanin hararar Rahul ya mayar mashi kafin yace "eh ga ku Musulmi ba mu ai takura ne a gun mu ko kaɗan ban son jin karatu"Rahul ya faɗa ganin irin kallon da Nur ke mashi yasa shi saurin sauya fira da cewa "wai nace ina budurwar ka malamar nan kwana biyu na ji shiru kabar ƙorafi a kanta"ɗan sosai ƙeya yayi kafin yace "wai Laila ?tana nan amman na jima ban kirata ba ko ta kira ni ban ɗauka"

Cike da mamaki ya tambaya "dan mi?"direct ya bashi amsa da "in ba haka nayi mata ba to lalle bazata taɓa bari na moreta ba "

Cikin nuna ƙin jin daɗin haka Rahul yace "Please Nur ka ƙyaleta tunda ka nada su Elli da Iki su kaɗai sun isheka kar ka ɓata yarinya mutane"saurin katse shi yayi da "no kar kayi ɓarnar bakin ka ai yanzu Nur bai sake alaƙa da wacce ba Virgin ba,tuni Iki ta buɗe min ido ashe suma mata kamar sabuwar mota ce wadda take dal a leda ba ɗaya take da wadda aka riga aka buɗe ba"galala Rahul yayi da baki yana kallon shi gira Nur ya ɗaga yace "Yes ko baka ga yanzu Elli bata gabana ba sai Iki?"kafin kace wani abu suka ji an banko ƙofa ,Esta ce cikin sleepinc dress sai wani karkaɗa jiki take kamar zata ƙalle.

Da sauri Rahul ya taso yayi huging nata yana mai jawota suka faɗa bisa godo,kamar yadda suka ba yau ma luluɓewa suka yi cikin bargo suna aikata masha'ar su sai nishi suke da fitar da numfashi tamkar su ɗaya ne cikin ɗakin.

Duk da ba yau ba ne farau ba amman bai hana Nur jin haushi ba,nan ya lalubi wayar shi ya shiga kiran Iki shiru bata ɗaga ba a na cikin haka kiran Laila ya shigo wacce kewa da gubar soyayya ta hanata barci.

Ɗagawa yayi ba tare da yace komi ba,ajiyar zuciya ta sauke tare da fara gaida shi da kyal ya amsa wanda sam yadda yake mata magana bai mata daɗi "dan Allah bbna kayi haƙuri kar ka sake yi min irin wannan hukunci kaji?"a yadda take magana kawai ya tabbatar mashi da cewa Laila ba ƙaramin so take mashi ba hakan ya sa yace "a'a miye na bani haƙuri kawai haka ne daidai kowa ya kama gaban shi tunda baki iya yi min ɗan ƙaramin abinda na saki Allah gama kowa da rabon shi"cike da tashin hankali Laila ta tari numfashin shi da cewa "ba fa haka ba ne bb abinda ka tambaya ne baida kyau"

"Mine ne baida kyau ?romance ne fah kawai kin fi kowa sanin yadda nake sonki ba zan iya cutar da ke ba,kuma Virgin naki nayi tanadin shi ne sai ranar tarihi ta first night ɗin mu"ko da Nur ya zo nan da zancen shi sai tunanin Laila ya kasu gida biyu ta yarda da shi ko kuwa a'a ....

****

Jikin momy ba a cewa komai sai hamdallah ga Allah dan yanzu tabar firgita sai mugayen mafarkai wanda sai tsakiyar dare aji ta ƙwala uban ihu in kuma an tambayeta sai ta fara kame-kame a ƙarshe tace babu komi.

Ɓangare guda kuma har an tsaida maganar auren Khalil da Maryam wanda jiran daddy kawai ake a saka ranar biki.Sosai Khalil ke murna da auren yayinda kuma gefe guda yake cikin ruɗani game da lamarin Maryam wani sa'in ta kan nuna mashi soyayya wanibi kuma tsana da hantara dan har ikirari take in ya bari aka ɗaura auren su sai ta zama ajalinsa a ƙarshe ta fashe da kuka.

William POV.

Tun lokacin da mother ta ɗaure shi da bai sake ganin ta ba,sai dai a mafarki inda duk abinda ke wakana a duniyar bil'adama yake zo mashi tiryan-tiryan.
Babu abin da yake ɗaga ma shi hankali sai auren da za ayi ma masoyiyyar shi.

Cike da firgici ya farka daga barcin da ya ke,karo na farko da yaji haushin mother domin ya san duk wannan tuggun ita ta ƙulla shi.

Lumshe ido yayi yana mai yin tunani akan wata formule ta tsafi da mother ta koyar da shi,a hanki ya fara motsa bakin shi tare da karanto ɗalasiman tsafi a take Maryam ta bayyana a jikin bango tamkar a tv.

Zaune take a cikin toilet ta haɗa kai da gwiwa sai gwanjin kuka take,kamar daga bisa yaji ta fara magana "Please mahaɗin rayuwata ka zo gare ni yanzu ka bar sona abaya a duk sadda na shiga toilet nakan ji kamar ina tare da kai yanzu kuma ka bar zuwar min gashi har ana son min aure da wanda ban so"ta ƙarashe maganar cikin kuka kafin kuma daga bisani ta miƙe ta nufi bakin mirror tayi tsaye tana kallon surar jikinta.

Hankalin William ne yayi mugun tashi ganin kyakkyawar surarta ta bayyana tarau ta yadda ya ke ganin komi na jikinta,so ya ke ya miƙe amman ya kasa a na haka ya tsinkayo Khalil yana bubuga ƙofar toilet ɗin.

Cike da so da ƙauna Khalil ya shiga bubuga ƙofar yana cewa "sweety kiyi sauri ki fito har mai kwalliyar da mai ɗaukar hoto sun zo"can cikin toilet ta ja wani uban tsuki kafin tace "na ƙi na fiton kum...."cak maganar ta tsaya sakamakon kanta da taji ya sara sai kuma ta ci gaba da cewa "ka jira ni honey yanzu zan fito da fatan dai har ka shirya?"cike da mamakin al'amari' Maryam  ya amsa mata da "eh"kafin ya fice daga ɗakin.

A ɓangaren William kuwa wani tuƙuƙin baƙin ciki mai game da ɓacin rai ne ya rufe shi,sakamakon ganin mother ta shige cikin jikin Maryam dan canza mata aƙida na yi ma Khalil biyayya .

A gagauce Maryam ta yi wanka ta fito sai wani rawar kai take irin na amare,mai kwalliyar ce ta

shigo nan ta tsantsara mata kwalliya kafin ta tayata zaɓen kayan da za ta fara sakawa.

Wata rantsatsar shadda bleu ciel Khalil ya shigo da ita wacce ta kasance iri ɗaya da ta jikin shi,miƙa ma Maryam yayi yana murmushi"ki saka wannan kin ga mun yi anko"maimakon ta karɓa sai wani shagala da ta yi da kallon shi,gira ya ɗaga mata yace "ya ko shirin bai yi ba?"dan sunkuyar da kai tayi tace "na ga kamin kyau ne ba kamar kullum ba"
"To in ba abun ki ba ko kin manta na kusa zama ango?"
"Haka ne"ta faɗa tare da karɓar kayan.

A babban falo aka shiga ɗaukar su hoto ,da ka gan su ka ga masoya irin yadda suke aika ma juna da kallon soyayya.
Cike da farin ciki momy ke kallon yaran nata sai murna take,a ƙasan zuciyarta kuma addu'a take "Allah kasa har a gama bikin nan fatalwar Suweiba ba zata zo min ba,ta yadda zan gwangwaje sosai"ba ta ita tunanin ta ba ta tsinkayo Suweiba a fuskar Maryam tamkar da ita ce ake ɗaukar hoto,har zata kawar da kai taga tana hararar ta .Bugun zuciyar momy ne ya ƙaru nan ta fara karanta duk addu'ar da ta zo bakin ta.

"Momy ki shigo ayi mana na family"cewar Maryam ta na mai sakar mata murmushi wanda momy ta gan shi kamar bakin tsoho babu haƙora,cike da tsoro ta girgiza kai alamun ba za ta je ɗin ba.
Fuska Maryam ta kwaɓe cikin sakuwa tana bubuga ƙafa tana mai cewa "ni dai ban yarda ba ki zo kawai ayi mamu"tashin hankali wanda ba'a sa mashi rana domin idon momy wata halitta daban ta hango a matsayin Maryam a take ta zube ƙasa a sume wanda yayi daidai da shigowar daddy.

*WAIWAYE....*

Alhaji Hamidine shahararren ɗan kasuwa ne wanda duk illahirin nahiyar Nijer ta san da shi,a maraɗi yake a zaune a wata unguwa ta masu hannu da shuni Ali Dan Sofo.
Matar shi guda tal Hajiya Turai,ƴaƴan su biyu maza Salis shine babba sai Sani wanda ya kasance ƙarami kuma Auta.

Lele da gata tare da sangarta su suka yi ma uwannan yaran ƙawa domin basu san wata wahala ba tun suna ƙanana har suka mallaki hankalin kansu suka yi aure.

Talatu ita ce ta kasance matar Salis shekarar su biyu da aure kamin Sani ya auro Suweiba

wadda tun watan auren su Allah ya azurtata da juna biyu saɓanin Talatu wacce ko ɓatan wata bata taɓa yi ba.

Samun cikin Suweiba shine farkon abinda ya fara jefa gaba tsakanin ta da Talatu domin ba ƙaramin ƙwallafa rai alhalin gidan suka yi ga Ɗan cikin ba,tun daga Alhaji ,Hajiya ,Salis uwa uba Sani wanda tun farko Allah yayi shi da son yara.

Cike da zullumi Talatu ta shiga kewaye cikin ɗaki domin samo ma kanta mafita,can tayi murmushi tare da cewa "yauwa doli na samu ciki ko kuma ke ma ki rasa naki iyee bari na kirawo ƙawalliya"bugu biyu ta ɗauka cikin kirarin da Talatu ta saba yi mata tace "Zahra tauraruwa mai haske duniya,um...wani taimako nike son ki min ki haɗa ni da malamin ki ko Allah sa na dace wannan karin na samu ciki"
Wata shewa Zahra ta rangaɗa kafin tace "ai dama na san kwanan zance tunda naji an ce Suweiba nada ciki na san da sai kin neme ni,amman fah magana ce babba kamar yadda na gaya maki tun farko dan aikin malam sai an bayar da jini na mutum ba dabba ba"ajiyar zuciya Talatu ta sauke kafin tace "yanzu dai sai gobe in mun haɗu".

★
Durƙushe suke gaban wani ƙaton arne ya na zayyano masu yadda abun zai kasance tare da gindiya sharaɗa masu ƙarfi a inda yake cewa "doli ne wanda zaki bada jinin shi ya kasance makusancin ki ne ma'ana kamar cikin familyn ku,sannan wacce zaki kawo takalmin nata tare da zanen da ta ɗaura a jikinta ya zamana zufar jikinta ta buge shi zata haukace ne domin muddin ta tsaya cikin hankalin ta asirin ki zai tonu"ko da boka ya zo da wannan batu sai Zahra tace "mi zai hana ki kawo na Suweiba tunda ita ma ta nada ciki kin ga shikenan"murmushi Talatu tayi "wlh kamar kin shiga zuciyata tunda takalmin mai ciki ake so ai shikenan ɗan cikin nata kuma sai aba dodani jinin sa na harbi tsintsu biyu da dutse guda"cewar Talatu kafin ta maida dubanta ga bokan ta sake jaddada ƙudirinta akan Suweiba.

Babu wani ɓata lokaci ya fara kiraye-kiraye ya na shafar wani faranti wanda ke ɗauke da ruwa a take Suweiba ta bayyana,alamu yayi masu da su leƙo cike da al'ajabi da kuma yarda da aikin bokan suke kaɗa kai ganin hatta jinjirin da ke cikin cikin Suweiba sun hango.Kuɗin gaske Talatu ta baiwa boka tare da yi mashi alƙawarin tukuici mai tsoka in buƙata ta biya.

Bayan sati guda da faruwar haka Talatu ta kashe cibiyar pampon ɗakin Suweiba da kuma na tsakar gida,babu a ko jima sai ga Suweiba ta fito da ɗaure gaba da kwandon wanka ta nufi toilet ɗin tsakar gida wacce a ciki a ka tanadi ƙaton tano na ruwa.

Ko minti biyu bata fara ba da wanka Talatu ta ɗauke zanen Suweiba ta kai ɗaki inda tuni Zahra ke jiranta.
Cikin dariya mugunta ta saka takalme guda na Suweiba a leda tare da zanen ta baiwa Zahra ita kuma ta fice domin kaima boka.

Da dare an haɗu a dining kamar yadda suka saba dukan ƴan gidan ke haɗuwa a ci abinci,nan ne fah Suweiba ke gayin an sace mata zane ɗazu Allah yasa ma ba'a gama da hijab ɗin ba.Sosai aka shiga tattauna maganar inda Talatu take cewa "ƙila bararoji ne masu kawo tallar maganin gashi ni sam hankalina sam bai kwanta da su"kamin wani ya tanka Suweiba tayi wata irin ƙara ta dafe ciki, kasancewar cikinta ya shiga wata takwas da ƴan kwanaki sai aka ɗauka ko naƙuda ce shiyasa aka kaita asibiti magani kawai aka basu suka dawo gida.

To tun daga wannan lokacin fah Suweiba bata ƙara samun lafiya ba,dama-dama ma Sani nayi mata addu'ar da ya saba tun da samu cikin domin neman kariyar ɗan cikinta.

Cikin dare gari yayi tsit Talatu ta fito ta shiga barbaɗa magani tare da ambaton sunan Suweiba sannan ta wurwurga wani dunƙulan abu ta jefa sama ta na mai cewa "kogon Kiresh wanda ke can kusan bangon duniya can zaki je Suweiba"ta na gamawa ta shige ɗaki.

Tun asubar farin taji haniya tsakar gida,fitowa tayi kafin ta kai da tambaya taji Sani na sake maimaitawa "wlh ko da na tashi ƙofar ɗaki a rufe take balle in ce fita tayi"
"Ka tabbatar kuma sai da ta shigo ɗaki sannan ka kulle ƙofa?"cewar Alhaji mahaifinsa"eh baba ni na shimfiɗar da ita ma fa"Sani ya ƙarashe maganar cikin rawar murya.

Abun mamaki tun daga wannan ranar babu wanda ya sake tambayar Suweiba kaf gidan in ka cire Sani wanda tun farko ya kasance mai riƙon addini shiyasa sihirin bai kama shi ba.
A duk lokacin da Sani yayi ma mutane maganar Suweiba sai suyi mashi ɗaukar mahaukaci hatta iyayen da suka haifeta sun manta da ita, wannan dalilin yasa Sani ya dage da addu'ar Allah ya bayyana mashi ita da nema mata kariya.
Addu'ar Sani ita ke neman kawo masu cikas wannan yasa Talatu ta biya ƴan daba suka kashe shi,Salis yayi kukan rashin ɗan uwan shi sosai dan har sai da ya zauce.

SUWEIBA POV.

Bayan sun gama sunnah aure sai take jin kamar gabanta na faɗuwa hakan yasa ta shaida ma mijinta Sani nan yace ta tashi suyi wankan tsarki sai suyi nafila budar bakinta sai cewa tayi "na gaji ko gobe na yi"nan take wani duhu ya fara rufe mata ido sai barci,ganin haka yasa shi ma Sani ya kwanta.

Kamar cikin mafarki taji ana kiran sunanta tare da yi mata raɗa a kunne,a tsorace ta tashi kawai sai ji tayi an cillata wani wuri mai ƙololuwar nisa.

Halitta da ta gani ga banta ne yasa ta fara ja da baya duk da wurin duk ciyayi ne da ƙayoyi,ba komai ba ne ta gani illa bayan wata tsohuwar aljana wadda gashin da ke jikinta ma kaɗai abun tsoro ne.

Wata naƙuda ce ta sauko mata gadan-gadan a take ta haifu ba ta shirya ba,kukan jariri shi ya katse ma mother bautar da take dan a duniya babu abinda ta ke so sama da ɗa.

Jin ƙamshin bil'adama yasa ta rikiɗa ta zama mutum kafin ta juyo inda Suweiba take cikin jini,da sauri mother ta ɗauki jaririn ta na kallo kafin ta yanke mashi cibiya tace "mi ya kawo bil'adama a kogon Kiresh wanda hatta aljanu ma suna shakkar shigowar sa saboda haɗarin da ke ciki?"maimakon Suweiba ta bata amsa sai kawai ta kece da dariya tare da rugawa a guje amman sai mother ta sa dogon hannunta ta maido da ita,kallon idon Suweiba kawai tayi ta fahimci sihiri aka yi mata da kuma wanda yayi mata.

Duk da Suweiba na cikin halin hauka bata manta kalmar shahada ba,nan ta shiga jerota kafin rai yayi halin sa sosai mother ta shiga damuwa dan lokaci guda taji ƙaunar su taimako guda tayi mata shine ta maidota duniyar bil'adama nan aka tsinci gawarta aka suturtata a ka kaita gidanta na gaskiya bayan anyi neman danginta ba a samu ba.

"William shine sunan ka ɗan mama ina sonka,zan reneka mu ɗauki fansa tare zan sa ka zama *MUTUM DA RIGAR ALJAN*"cewar mother ta na mai baiwa William nono a nan take ya kama ya fara sha.

TALATU POV.

Shiru-shiru tana jiran samun ciki amma har an kwashe 5ans(5years)ko dakwaye ba tayi ba,sai a shekara ta bakwai ne ta samu ciki wanda ke da mugun laulayi da azaba gefe guda kuma cin kuɗi dan kullum cikin ciwo take wannan yasa duk kuɗin familyn yayi ƙasa wanda har ya kai da Salis fara neman aikin gwamnati yayi nasara samu kuwa domin yanzu tsufa ya zo ma Alhaji kasuwanci ya aje sai ya zamana duk nauyin su ya koma kan Salis.

Shekarar da Talatu ta haifi ƴar ta Maryam a wannan shekarar aka saida rabin gidan da suke zaune Salis ya sayi wani gida daban saboda tsangwamar da Hajiya ke nuna ma Talatu.

```Wannan ne ɗan ƙaramin tarihin```

CIGABAN LABARI....

Cikin tashin hankali daddy ya ƙaraso yana "subhanallahi kar dai a ce ciwon ne ya dawo?"kasancewar momy sadda tana ƙarama tayi rashin lafiyar farfaɗiya.
Ruwa masu sanyi Maryam ta zuba mata aiko ta farka ta na mai ɓoye bayan daddy.....

*****

Cikin rashin madafa Laila tace "ok zan yi amman sai ka min alƙawali banda sex ɗin dai"kwanciya Nur ya gyara ya fara kalalameta da daɗin baki tare da ƙara shimfiɗa mata gada zare "ok naji amman doli sai ranar lundi tunda gobe weekend ne,amman kuma ka san ba a school ɗin ku zan je ba ko?"
"Eh akwai wani gida daban in baki ra'ayin nan ɗin"
"Ok sai da safe"cewar Laila ba tare da ta jira cewar shi ba ta kashe kiran jin motsin Abba.

Saurin liƙe ido tayi kamar mai barci sai abinda bata sani ba hasken wayar ta ya gama tona mata asiri, girgiza kai Abba yayi tare da kashe masu hasken ɗakin.

Ajiyar zuciya ta sauke tare da ɗaukar wayar ta tura ma Nur message na jaddada ƙauna da soyayyar da take mashi.
```

A ɓangaren Nur ƙuwa ba su wani jima da gama waya ba kiran Iki ya shigo,cikin zumuɗi ya ɗaga suka fara firar soyayya mai cike da baɗala wanda hakan yasa shi shaf ya manta da wasu wai Esta da Rahul.

Ranar Lundi (Monday) ƴan magana kan ce ko mushe na tsoronta, wannan yasa duk ɗalibin ƙwarai kan zuwa kan lokaci.
Shiri Laila take kamar ba gobe duk wani lungu da saƙo na jikinta ta feshe shi da wani arnen turare.

Fitowar ta falo rataye da bag ɗin school yayi daidai da shigowar Abba domin har ya fita ya dawo yayi mantuwa,cike da ɓacin rai da kuma mamakin halin da ta tsiro kwana biyu yace "duk turare ne kika baɗa kamar ƴar bori kuma wai a haka zaki fita?"

Cikin i'ina ta sharo ƙarya "Abba kwalbar turaren ce ta fashe shine na goge da hijab ɗina amman bari na canza wani,ƙila dan ina mura ne shiyasa ban ji hawan kan da yayi ba kuma Abba ai ka san ban saka turare mai ƙamshi wannan...."ɗaga mata hannu yayi tare da mata nuni ta koma ɗaki ta canza.

Nur kwance bisa ɗakin wani abokin shi yana jiran Laila sai duba lokaci ya ke ƙarfe tara suka yi alƙawali yanzu kuma duka 7 na safe da ƴan mintina.
Tsuka ya ja kafin ya miƙe ya jawo plate ɗin indomi ya fara ci ya na korawa da jus,kamar daga sama yaji ana bubuga gida lokaci guda kuma text ya shigo wayar shi " ```gani a ƙofar gida ka zo ka buɗe min kar wani ya gan ni```" har da wani ihu Nur yayi kafin ya nufi hanyar waje........
[18/10 à 14:35] MRS SADAUKI 💫: *MUTUM DA RIGAR ALJAN*👹

*Gajeren labari...*
Story
and
Written by
*MRS SADAUKI 💫✍️*
{Cham rose💞}
Dedicated to *PRINCESS AYSHATOU*

☀️ *FIRST CLASS WRITTERS ASSOCIATIONS*☀️

BISMILLAHI RAHMANI RAHIM.

Page 30-31

Murmushi Nur ya saki lokacin da idon shi suka yi tozali da Laila cikin doguwar riga ta abaya,hannunta riƙe da bag.
"Na fah zata ba zaki zo ba"cewar Nur ya na mai matsawa dan ba Laila hanyar hucewa,shigowa ta yi ta na mai cewa "sai gashi kuma na zo"ta faɗa cikin cool voice tare da nufar hanyar ɗakin.

Da ta shiga sai kuma ta ƙara da
"Waooo amman ɗakin nan ba ƙaramin haɗuwa yayi ba"rungumeta yayi ta baya yana mai cewa "Allah baby?"kai ta ɗaga alamun eh,sunkuyo kanshi yayi gefen wuyanta yace "ai gidan mu sai yayi wannan kyau "murmushi mai sauti Laila tayi tace "kaiii amman naji daɗi ko gidan ku na Sonisi zamu zauna?"cike da mamaki Nur ya juyota da alamun tambaya fuskar shi yake kallon ta,"eh mana ko ka manta kace min duk gidajen mahaifin ka na Sonisi yafi kyau?"murmushi yace "na manta shaf na zata ba mu taɓa hirar ba ne,am....bari na kawo maki jus".

"Kar ka ɗauko min na mango nafi son goyave"cewar Laila ganin ya nufi frigo,waigowa yayi yace "kamar kin san ko shi zan ɗauko maki,ni Mango ne favorite ɗina"ya faɗi haka yana mai tsiyaya mata jus ɗin a kofi.

Kusa da ita ya zauna cikin salon su na ƴan duniya ya shiga ɓalle mata butanin riga yana mai cewa "ya kamata ki cire wannan ki ɗan sha iska"sunne kai Laila ta yi ta na ɗan noƙewa shi kuwa Nur har jikin shi ke rawa yana maganar zuci"yarinya kin shigo hannu tunda har tsotsayi yasa kika kawo kan ki".

Cikin mintina da ba su fi talatin ba Nur ya karɓe budurcin Laila,cikin murya mai nuni da rarashi ya fara mata magana "miye kuma baby?ina ce dai ko auren muka yi ni ne zan karɓi Virgin naki ko?to miye abun damuwa a nan ki yi shiru please kukan tamkar narkarka dalma nake jin shi a zuciya"wani murmushi ta saki wanda ba ta san lokacin da ta yi shi ba kafin ta shafi sajen fuskar shi tace "Nur ina sonka so marar misaltuwa zan iya yin komai a kan ka ciki har da kisan kai,Nur ban taɓa sanin haka rayuwa ke da daɗi ba sai yau da na kasance tare da kai kuma ina fatan ci gaba da kasancewa da kai har ƙarshen rayuwata ko ta halin ƙaƙa ne"tana gama faɗin haka ta shige cikin ƙirjin shi,wani abu Nur yaji yana shiga jikin shi wanda ya kasa tantance ko mine ne.

LAILA POV.

Cike da jin haushi ta koma ɗaki ta canza hijab kafin ta fito da sauri ta nufi ƙofar gida,cikin sa'a kuwa ta samu abun hawa har bakin get ɗin makarantar su ya sauketa.

Tana fitowa ta tsinkayo Zee da sauri ta ƙarasa gunta tare da rungumeta cikin murna tace "ƙawata yau akwai labari "ɗan tureta Zee tayi "ke ni sakar ni kin wani ruƙunƙume ni sai kace kin samu Nur"cewar Zee tana ɗan ja da baya,"to ai akan shi ne nake son baki labari kin ga abaya nan nazo da ita in an jima zuwa ƙarfe tara nake so ki raka ni wajen shi"cike da mamaki Zee tace "mi kuma za ki yi wajen sa baki jin tsoro ne?"maimakon Laila ta bata amsa sai kuma ta ɗauko mata wani zance "ke ni ba ma wannan ba wlh jiya nayi mafarkin Nur na biyata da gudu ga wani ƙaton ƙadangare a hannun sa wai sai ya cilla min shi,sau wajen uku yana tullo min shi ina kauce wa har sai ya kusa faɗowa jikina"waro ido Zee tana cewa "Allah kyauta ya kuma kare ki daga sharrin shi,muje cikin aji please ki koya min math".

Cours ake amman hankalin Laila sam bai jikinta,tunani kawai take yadda moment ɗin su zai kasance da Nur ana haka har lokacin fita shan iska yayi.

Hijab ɗinta ta cire ta ɗora doguwar rigar abayarta kafin ta fito bakin titi jiran abun hawa,sai da ta sha tsayuwa sosai kafin wata farar mota ta tsaya kusa da ita.

"Ma chérie Laila ashe ki na nan?har na wuce na tsinkayo ki"cewar wata farar mace lokacin da ta zuge gilashin mota,kallon inda ta santa Laila ta shiga yi amman sam ta kasa tunawa a haka dai ta amsa mata ta ƙarashe da cewa "sai dai ban gane ki ba"murmushi tayi mata tace "ki shigo na aje ki inda zaki"cikin zumuɗi Laila ta shige gidan gaba ita kuma ta ja mota suka tafi.

Sai da suka yi ɗan nisa ta samu wuri ta yi parking tana mai kamo hannun Laila tare da yin magana cikin wani yare tun daga wannan lokacin Laila ba ta sake sanin inda take ba sai tashi tayi ta ganta a gida.

Kai ta dafe ta na son tunawa da abin da ya faru amman ta kasa,abu guda kawai ta tuna shine ta canza kaya izuwa abaya zata wajen Nur "to amman ya aka yi na kasa tuna ko na je ko ban je ba wash "ta faɗa tare da ƙara dafe kanta.

Paracétamol ta ɓalla ta sha ko ta samu relief tare da ɗan kishingiɗawa. Wayarta ce ta bado haske alamu kira na shigowa,lambar Nur ce ke yawo a jikin screen ɗin.Sai da ta kusa katsewa sannan ta ɗauka,kamar kullum da sallama bakinta amsawa yayi kafin yace "na gajiyar da ke sosai ko?kiyi haƙuri baby har magani na zuba maki a jus dan kar ki wahala sosai,am...ya maman ta lura da canjin ki ko kuwa?"cewar Nur wanda ke ta zuba kamar kanya,shiru Laila ta yi ta na jin zuciyarta na bugun tara-tara sam ta kasa tuna komai ,ga Nur na yi mata wani zance da alamu ta je gidan na shi,cikin i'ina tace "canjin mi?"
"Tafiyar ki mana ko kin manta kince zafi kike ji ba zaki iya tafiya daidai ba?"jin Laila ba tace komai ya ci gaba da cewa "humm!  Amman fah baby kin haɗu sai dai raki ko dayake ba laifin ki ba ne fitar virginité ne da wuya,ki kula da kan ki sosai ta yadda babu wanda zai gane zan tafi na yi sallah"ƙit ya katse kiran.

Shaɓe-shaɓe haka fuskar Laila ta ɓace da hawaye, "shikenan na ci amanar iyayena kaicona ni Laila mi yasa ka aikata haka gare ni Nur ?kenan ka san ba zan iya ba shine ka zuba min magani wayyo na shiga uku"ta miƙe tsaye ta na yarfe hannu kafin ta shiga saffa da Marwa ta na tunanin wanda zata gayawa,Zee ce ta faɗo ranta hakan yasa ta ɗauki waya ta kirata bugu ɗaya aka ɗaga.

Ba tare da ko Laila  ta yi magana ba Zee tace "ƙawa yanzu kam nake shirin kiran ki da sanar da ke fassara mafarkin ki,wai kinji ashe mafarkin ƙadangare ciki ne to ki dai yi hank...."ba ta ƙarasa faɗa ba Laila ta saki wayarta ai ko ta fashe tare da ɗokewa lokaci guda .

Ba ta san ta ƙwala ƙara ba sai da ta ga umma a guje ta shigo ɗaki ta na mai tambayar ta lafiya,ɗagowa jajayen idonta ta yi ta kalli mahaifiyarta ta wani tausayinta ne taji ya tsarga mata,ya umma zata ji in na gaya mata nayi fatali da tarbiyya da ta bani na aikata saɓo mafi muni a duniya?Laila ta tambayi kanta a zuci,kusa da ita umma ta je ta dafata cikin tausashashiya murya ta sake tambayar ta "umma wata ƴar classe ɗin mu ce ta rasu kuma fah ko ɗazu taje makaranta"shine abin da ta samu bakinta na faɗa.

"Allahu Akbar duk mai rai mamaci ne Laila Allah jiƙanta,addu'a ya kamata kiyi mata ba kuka ba"cewar umma ta na mai fita waje dan fidda abinci.

ESTA POV.

Cike da jin daɗin samun nasara take shiryawa cikin wasu riga da wando na jeans,bata wani ɓata lokaci ba ta ɗauki makulin mota bata zarce ko ina ba sai school ɗin su Laila.

Kasancewar ta taɓa ganinta a hoto shi yasa bata wani ci wuya wajen ganeta ba,gada zare ta shimfiɗa mata ta ɗauki Laila a mota da zumar rage mata hanya sai bayan sun yi nisa ne tayi magie ta koma sak Laila kafin kuma ta mayar da Laila can gidan iyayenta tare da hura mata iskan da ya haifar mata cutar mantau.

Esta ta je gun Nur a matsayin Laila wadda cikin hikimar su ta *JINN* ta mayar da kanta budurwa, wannan dalilin Nur ya sameta a Virgin .

1semaine plus tard(1week later)

Abubuwa dayawa sun faru ciki har da rashin zuwan Laila makaranta sakamakon damuwa da ta ɗora ma kanta,ba ta cin komai sai ruwan kunu wannan dalilin yasa olser ta ƙara yi mata mugun kamu da ta sha kunun sai amai in kuma aka matsa mata ta ci abinci a ƙarshe sai ta rinƙa jin tashin zuciya wannan dalilin yasa Laila ƙara fita haicinta domin ta hakiƙance ciki ne da ita.

Babu irin yadda Abba da umma ba su yi ba dan kaita asibiti amman sai ta zille sai dai ta sha magani duk gudun kar asirinta ya tonu.

A ɓangaren Nur kuwa ya kira lambar Laila yafi sau ɗari kullum amsa guda ce a kashe.
Yau ma ya na zauna sai gwada wa yake Esta da Rahul suka shigo ɗauke da shopping ɗin da suka yi.

Cikin jajantawa Rahul yace "wai har yanzu lambar bata shiga ba ne?ko fushi take da kai?"huci Nur ya sauke yana mai cewa "a kashe take har yanzu,yah har kun dawo?"wannan karon Esta ce ta amsa mashi da "eh"ta na mai juyawa dan komawa ɓangaren su.

Damuwa da ƙunci su ne suka taru suka yi ma Nur yawa,wanka yayi ya ɗauro alwala tare da jero nafila raka'a biyu a sujada ƙarshe ya daɗe yana nema Allah gafara kafin ya ɗago fuskar shi duk hawaye.

Karatun ƙur'ani ya fara cikin kwanciyar hankali sai dai mi wani irin ihu ya ji daga toilet ana cewa

"kar ka ƙona ni tunda ban yi ma laifin komai ba"tabbas ko tantama babu murya Rahul ce yake ji kuma yana fitowa daga wanka shi ya shiga.

Kafin Nur ya kai ga magana sai ga Elli ta shigo ɗakin kamar an cillota "na shiga uku Nur ashe Esta ba bil'adama ba ce *Aljana* ce sai yanzu n..."Nur bai bari ta gama faɗin maganar ba ya bangaje ya fita da gudu......

****

Momy na ƙoƙarin ɓoyewa bayan daddy yayin da Maryam da Khalil ke ƙara matsawa kusa da ita,cikin fushi Maryam tace "daddy ka gani ko wai guduna take"cike da mamaki daddy yace "miye kuma haka Talatu?ƴar kice fah"leƙowa momy tayi tare da sauke ajiyar zuciya ganin Maryam ta koma daidai.

Shagulgulan biki ake ta gudanarwa,tuni amarya ta shiga lalle wanda sai da aka sha daga kafin ta yarda.Sosai mutane ke mamakin Maryam yadda jiya ta yi ta rawar kai wajen zaɓen kayan da za ta saka ranar briday yayin da kuma yau take faɗin ba ta son auren.

Dangi na nesa da na kusa duk sun hallara,ƙannan Rakiya wato mahaifiyar Khalil wadda take yaya ga momy duk sun zo yayin da shi kuma Khalil ke shirin tafiya Zinder can garin iyayen shi dan yi taron bikin shi a can.

Daƙyar ya samu ganin Maryam wacce tasha kyau har ta gaji,an yi mata lalle da kitso sai wani ƙamshin amare take fitarwa.

Sai da Khalil yayi sumen wucen gadi dan ruɗewa yayinda zuciyarsa ta kwaɗaita ma shi shafar lallen hannunta,cikin gajiya da kallon ƙuren da yake mata ta ɗago kai idonta ne ya sauka cikin nashi.Wani irin shock yaji mai game da gubar sonta har bai san lokacin da ya kamo hannunta ba, ajiyar zuciya ya sauke  "baby zan tafi Zinder na zo ne mu yi sallama"ya faɗa yana mai jan yatsun hannunta,rarau da ido tayi kamin tace "tafiya kuma?sai yaushe ka dawo kenan amman ka san zan yi kewarka"

"Kar ki damu baby an kusa fah kawo min ke gidana so kar ki damu ki min addu'a"Khalil ya faɗa yana gyara kitson da ya zubo ta gefen fuskarta,wasu irin hawaye ne taji sun cika mata ido kafin

su zubo sharrr ga kumatunta.
Janyo ta yayi zuwa jikin shi da niyyar bubuga mata baya amman sai ta wani hankaɗa shi baya,hannu ta nuna ma shi alamun kashedi tare da zaro ido sai kuma ta juya ta bar Khalil sake da baki.

WILLIAM POV.

Tun daga ranar da ya samu Maryam a toilet tana wanka bai sake ganinta ba,sosai ya shiga damu yayi iya ƙoƙarin shi na ya kwance amman ya kasa.

Rumtse ido yayi yana jin zuciyar shi na ɗunguza shi daga akan abin da take raya mashi,ba komai ba ne sai musulunta "tabbas lokaci yayi da zan musulimta ba tare da na yi duba da gargaɗin da mother ke min ba,ta wane dalili ma zan ci gaba da zama a nan alhalin ni ɗin bil'adama ne?wai mi yasa ma ban yi wannan tunanin tun da wuri ba sai yau? "William ya faɗa a bayyane,zuciyar shi ta bashi amsa da "har yanzu lokaci bai ƙure maka ba William ka musulumta"ya na gama wannan tunanin bai san lokacin da bakin shi ya fara furta ```ASH-HADU AN LA'ILAHA ILALLAH WAHADAHU LAASHARI KALLAH,WA'ASH-HADU ANNA MUHAMMADAN ABDAHU WAR RASULULLAH``` wani irin sanyi ne ya fara ratsa sansar jikin shi yana mai jin tamkar an cire mashi ƙaya...
[20/10 à 10:18] MRS SADAUKI 💫: *MUTUM DA RIGAR ALJAN*👹

*Gajeren labari...*
Story
and
Written by
*MRS SADAUKI💫✍🏻*
{Cham rose💞}
Dedicated to *PRINCESS AYSHATOU*

☀️ *FIRST CLASS WRITTERS ASSOCIATIONS*☀️

---

BISMILLAHI RAHMANI RAHIM.

Page 32-33

Laila na kwance a ɗaki Abba ya aiko kiranta,jiki ba ƙwari ta tashi.Ta na zuwa ta gaishe shi tare da cewa "Abba ga ni"ɗan dubanta yayi ya sauke ajiyar zuciya kanan yace "Laila ita rayuwar duniya da kike ganinta komai Allah ya riga da ya tsara shi,dan haka ina son ki ɗauki abin da zan faɗa maki a matsayin hukuncin Allah.Tun jiya na yanke shawarar haɗa auren ku ke Zaharadeen abokina ,dama tunda matar shi ta rasu bai sake aure ba to ina so ki zama silar dawowar farin cikin shi"tunda Abba ya fara magana gudun zuciyarta ya ƙaru,ba wai na auren ba ne a'a kawai kalmar da zata gayawa mijin bayan aure in ya tambayeta ina ta kai budurcinta.

"Kin yi shiru baki ce komai ba"muryar Abba ya maido da ita daga tunanin da take,can ƙasan maƙoshi murya na karkarwa tace "to Abba in shaa Allah"cike murna yace "tashi kije Allah yayi maki albarka".

ABBA POV.

Cike da murna ya samu abokin shi da maganar,"haba ta yaya zan auri ƴar ka ?ita fah kamar ƴar cikina ce sam wannan magana ka barta please"cewar Dr Deeni.

"Toh shine mi dan ka auri Laila?na fah gayama auren nan babu fashi tafiya zan yi na samu gwagwo na shaida mata in ma dai *JINNU* ke bisa kan ka doli su sauka"Abba ya faɗa tare da miƙe har ya kai bakin ƙofa ya tsinkayo murya Dr yana cewa "ita Laila ɗin ta yarda?"murmushi kan fuskar Abba ya bashi amsa da "eh"sai kuma ya dawo suka fara tattaunawa akan yadda bikin zai kasance.

*Zaharadeen* shine cikakken sunan shi,mahaifan shi sun rasu tun yana ƙarami,ya taso ne hannun yayar baban shi wacce yake kira da gwagwo, Zaharadeen dogo amman ba siriri ba,ya nada haske ba laifi,fusakar shi rond ce mai kewaye da kwantacen saje baƙi wuluk.

Abotar su ta faro asali ne lokacin da ya banke Abba to tun daga ranar jinin su ya haɗu duk da cewa ba sa'anin juna ba ne amman tasu ta zo ɗaya kuma ƴan karin magana na cewa yaro da kuɗi abokin manya.

Bayan Dr yaje gida ya shiga tunanin yadda zaman su zai kasance shi da ƴar abokin nashi,in yace bai sonta yayi ƙarya amman a ganin shi kamar abun kunya ne.Kanshi ya fara sarawa ga wani irin bugu da zuciyar shi ke yi a hankali ya buɗe baki yana cewa اللَّهُمَّ لَا سَهْلَ إِلاَّ مَا جَعَلْتَهُ سَهْلاً وَأَنْتَ

تَجْعَلُ

الْحَزْنَ إِذَا شِئْتَ سَهْلاً

```Allaahumma laa sahla illaa maal ja'altahu sahlan wa Anta taj'alul-hazna 'izaa shi'ta sahlan.```

Sai da ya nanata wannan addu'ar fiye da sau uku yana mai tawasali da Allah dan neman yarda shi da kuma kawo mashi komi cikin sauƙi.

Toilet ya shiga ya na mai sakar ma kanshi shower,saukar ruwan a kanshi ba ƙaramin taimaka mashi suka yi ba.A hankali ya fara sauke ajiyar zuciya yana mai jin kamar an sauke mashi dutse.
Wankan soso da sabulu yayi gami da ɗauro alwala kanan ya fito,wayar shi ya ɗauka ganin ta na bado haske alamun saƙo ya shigo.

```Ga lambar Laila nan please ka kira ta zan so ace kun ƙulla soyayya kafin auren``` shine abinda saƙon ya ƙumsa dariya yayi kafin yayi enregistrer (saving)lambar da *Dear*.

LAILA POV.

Tunda Abba ya gaya mata maganar auren komi ya ida dagule mata,sosai take cikin tashin hankali wanda ake kira tsaka mai wuya.Ta kira lambar Nur fiye da goma amman bata shiga,tun tana gwada kiran har ta daina dan zuwa yanzu ta yarda da zancen ƴan magana ```an ci moriyar jiki an yadda gangarsa``` ganin dai abun bai fisheta yasa ta ɗauro alwala ta fara jero nafilolu,sai da ta sallamce ta ɗaga hannu sama tana roƙon Allah

اللَّهُمَّ إِنِّي عَبْدُكَ، ابْنُ عَبْـدِكَ، ابْنُ أَمَتِـكَ، نَاصِيَتِي بِيَدِكَ، مَاضٍ فِيَّ حُكْمُكَ، عَدْلٌ فِيَّ قَضَاؤُكَ، أَسْأَلُكَ بِكُلِّ اسْمٍ هُوَ لَكَ، سَمَّيْتَ بِهِ نَفْسَكَ، أَوْ أَنْزَلْتَهُ فِي كِتَابِكَ، أَوْ عَلَّمْتَهُ أَحَداً مِنْ خَلْقِكَ، أَوِ اسْتَأْثَرْتَ بِهِ فِي عِلْمِ الغَيْبِ عِنْـدَكَ، أَنْ تَجْعَلَ القُرْآنَ رَبِيعَ قَلْبِي، وَنُورَ صَدْرِي، وجَلَاءَ حُزْنِي وذَهَابَ هَمِّي

*Allaahumma innee abduka, ibnu abdika, ibnu amatika, naasiyatee biyadika, maadin fiyya hukmuka, adlun fiyya ƙadaa'uka, as'aluka bikulli ismin huwa laka, sammayta bihi nafsaka, aw anzaltahu fee kitaabika,aw allamtahu ahadan min khalƙika, awista'sarta bihi fee ilmil-gaibi indaka, an taj'alal-Qur'aana rabee'a ƙalbee, wa noora sadree, wa jalaa'a huznee, wa zahaaba hammee*

Tana gama shafawa ta raɓa gefen Rahila wacce ke ta sharɓar barci ta kwanta,lumshe ido tayi tana jin wata nutsuwa na shigar ta  a hankali kuma duk abinda ya faru ya dawo mata akai.

A fili ta furta "tabbas ban je wajen Nur ba amman wacece wannan wadda na haɗu da ita🤔"kafin ta kai ga samo amsa text ya shigo ```Zan kira ki yanzu Zaharadeen ne``` tana gama karantawa kiran shi ya shigo.

"Assalamu alaikum"shine abinda ta furta lokacin da ta ɗaga kiran,"wa'aleykum salam,da fatan ban tashe ki ba dai ko?"Dr ya faɗa "a'a"ta bashi amsa.
Ajiyar zuciya ya sauke bayan shirun da ɗan ratsa kafin yace "Abban ki yayi maki bayani ko?"sai da gabanta ya bada rasss kafin ta amsa da "um..."wata tambayar ya ƙara jefo mata wadda ta sakata yin dariya bata shirya ba "ki na sona?kin yarda zaki auri tsoho?"ɗan tsagaita dariyar tayi tace "ina tsohon?"a yadda tayi maganar cikin barkwanci yasa shi jin daɗi wanda har hakan ya kasa ɓoyiwa yace "ga ni mana ko baki san zan iya haifar ki ba inda an yi min auren wuri"turo baki gaba tayi a shagwaɓe tace "sai kuma aka yi rashin sa'a ba ayi ma auren da wuri ba,ni ba ma wannan ba duka-duka shekarar ka nawa ma?"waro ido yayi kamar ta na ganin shi yace "saba'in da bakwai"faɗar haka yasa Laila ƙara fashewa da wata dariya har da riƙe ciki,shiru yayi yana sauraren yadda sautin dariya ke fitowa gwanin sha'awa lumshe ido yayi yana jin sonta na shigar shi.

Buɗe ido yayi jin tana magana "kace ka kai sa'ar kakana?"cewar Laila tana mai kuma yin murmushi mai sauti,"eh kamar yadda ke kuma kike sa'ar kakata Kulu"bubuga ƙafafu ta shiga yi cikin shagwaɓa tace "Allah kiyaye min ni yarinya ce sharrr".
Fira suka yi tayi tamkar sun wani jima a fagen soyayya.

NUR POV.

Kwance yake a bisa tabarma a sandare tamkar gawa,gefe guda mahaifiyar shi ce ke kuka yayin da baban shi ya shigo shi da wani malami.

Ba a wani ɗauki lokaci ba malamin ya fara yi mashi barbaɗen magani,tare shafa mashi mai a goshi.Da zai tafiya kuma ya bada wasu ƙullin magani na wanka da na hayaƙi sai na shafawa,bayan baba ya dawo daga rakiyar malamin ya dawo ya zauna bisa lumtsetsiyar salon ɗin da ke ɗakin.

Tagumi ya zuba yana kallon tilon yaron nashi wanda shi da gawa babu banbanci,duban matar shi yayi yace "Ni fah sai nake ganin tamkar ciwon likita ne ba na gida ba,duba ga yadda muke ta kashe kuɗi a banza amma har yanzu babu wani canji ko mu kai shi asibiti?"majina maman ta fyace haɗe da goge hawaye tace "ba ka ji yadda abokiyar shi ta faɗa ba?tace soyayya suke shi da wata aljana ba tare da ya sani ba shine ranar da asirin ta ya tonu ya zube nan"kai kawai baba ya jinjina sannan ya sake cewa "mu dai jaraba na likitan ƙila shock ne ya kama shi" da "toh" ta amsa mashi.

***

Biki bidiri,banda shagulgula babu abin da suke.Yau ta kama daren biki gobe ɗaurin aure Amarya da ƙawayenta sai fira ake,Nadiya da Karima a nan za su kwana shiyasa aka watse aka barsu.

"Ku san wani abu?ni wlh ban son Khalil William nake so shi yafi dacewa da ni"cewar Maryam,a tare Karima da Nadiya suka yi karon baki wajen cewa "wanene William kuma?"yamutsa fuska tayi tace "ashe har yanzu ban baku labarin shi ba,to shi ɗin massoyina ne na mafarki hummm ina sonka my willi muaah"gama rufe bakinta ke da wuya suka ji wata murya mai sanyi da taushi yana cewa "Ki kwantar da hankalin ki baby muddin ina raye ba ki da wani miji bayan ni"wata irin ƙara suka saki su duka in ka fidda Maryam wacce ke murmushi tana tunkarar inda yake a tsaye,ƙanƙame Nadiya Karima tayi suna mai fashewa da wani kuka domin su sam ba su ga William ba murya shi kawai suke ji.

Shigowar mutane ɗakin yayi daidai da ɓacewar Maryam,cikin tashin hankali Nadiya ke yi masu bayani dan ita Karima tuni ta suma.
Zufa ce ta kariye ma daddy yayin da momy ta ɓarke da wata irin dariya sai faɗi take " ABIN DA KA SHUKA SHI ZAKA GIRBA(Haj Maryam Sakatare book ɗin nan naki ya faɗakar) wuuu ni ce nan da kaina na haukata Suweiba a ƙarshe na kasheta ita da ɗan cikinta,kaiiii ashe shi bai mutu ba ! eh bai mutu ba!wayo Allah da gaske baka mutu ba hahhh"ta na faɗar haka ta shiga kewayen ɗakin tana dube-dube kamar mai son ganin wani abu.

Cikin wannan zullumi duk wanda ke gidan ya kwana a washegari
Duk gari ya harkaɗe da ɓatan Maryam da kuma haukan momy wanda suratan da take sam babu dadɗin ji,faɗar irin tashin hankalin da daddy ya shiga ɓarna baki ne dan abu uku suka shiga yi mashi gizo ɓatan Maryam,haukan momy uwa uba sunan Suweiba da yake son tunawa amman ya kasa.

Ƴan ɗaurin aure da ƴan biki sun cika gida,babu abin da ake sai jajanta ma juna gefe guda kuma ana kankamar Khalil wanda sam hankalin shi bai jikin shi.

Haukan momy ne ya motsa nan ta fara zayyano irin muggayen ayyukan da ta yi da uwanda ,gaban Hajiya Turai (uwar Salis sarakuwa ga momy)ne ya faɗi jin ta ambaci sunan Suweiba da Sani,nan komi ya dawo mata a kai ta tuna wace ce Suweiba.

Tuƙe momy Hajiya ta yi idonta duk sun fito,nan ta shiga jijigata tana cewa "gidan uban wa kika

kai mi suruka da jikana?yanzu dan rashin imani har ƙanan mijin naki sai da kika kashe ?to yau ke ma sai na kashe ki"ta ƙarasa maganar ta mai kama maƙogwaron momy.

Ganin Hajiya za tayi kisan kai yasa mutane suka shiga ɓanɓare mata hannu ,dakyar suka ceci momy.Wata dariyar ta sake sheƙewa da ita tana nuna Hajiya Zahra wace shigowarta kenan "yauwa ƙawalliya gaya masu ke kika raka ni gidan boka mu ka amso maganin da ya hauka Suweiba hhhh"Hajiya Zahra na jin haka ta juya da zumar fecewa daddy ya daka mata tsawa sumi-sumi ta dawo ta zauna a wurin da yayi mata nuni.

Malam Rabi'u ne ya shigo, kasancewar an yi mashi bayan tun kafin ya zo yasa shi fara karatu. Wani irin gurnani momy ta fara yi tana cewa "malam kar ka ƙona ni domin wannan matar babu abin da ya dace da ita sai azaba"nan mother ta shiga fallasa asirin momy kafin daga ƙarshe tace "ko kashe ni zaka yi ba zan fita daga jikin ta ba "karatu malam ya shiga yi wanda ya galabaitar da mother cikin ƙaraji da azaba take magana "zan fita amman dan Allah kar ku raba ni da William ina son shi ni na raine shi"

"A'a wlh ba zan bar maki jikana ba Malam ka taimaka kace ta fito min da jika"cewar Hajiya tana kuka,riƙeta daddy yayi yana kwantar mata da hankali.

Sai da aka sha daga sosai kafin mother ta haƙura ta bayyanar da William,ashe dama ko da ya ɗauki Maryam bai tai ko ina ba suna cikin gidan.

Duk mutanen wurin kallon ikon Allah suke ganin William gefe guda kuma Maryam ce sai riƙe mashi hannu take.

Hajiya Turai kuwa kasa motsawa tayi dan ganin tsantsar kamar da yayi da Sani.
Hannu malam ya aza bisa kan William ya shiga karatu ,wani baƙin abu ne ya shiga amayarwa kamar ran shi zai fita shi kuma malam sai ƙara ƙaimi yake.

Ba ƙaramar galabaita William yayi ba dan sai da ya amayar da nonon da mother ta bashi tun yana jariri wanda shine silar kasancewr shi *MUTUM DA RIGAR ALJAN*

Kamar ɗokewa ruwa haka momy ta dawo daidai bayan tayi atishawa uku,kallon mutane ta shiga

yi bisanin ta ƙura ma William ido wanda ke kwance yana fitar da numfashi.
Motar ƴan sanda ce ta tsaya,tisa ƙeyar momy aka yi ita da Hajiya Zahra.So take tayi magana domin yafiyar daddy amman bakinta yayi mata nauyi,idonta na zubar da hawaye aka tura su cikin mota.

Da taimakon Khalil William yayi wanka,ya shirya tsaf cikin wata dakakiyar gizna fara sol wadda ta kasance ta Khalil ɗin ce.
Dama tun can ya karɓi kalmar shahada,jaddada masa ita kawai aka yi tare da sauya masa suna.
Mutanen da suka yi saura aka zazauna aka ɗaura auren Mohammed Sani tare da Maryam Salis akan sadaki ƙanƙane.

Sosai Khalil yayi jarumta wajen kwantar da hankalin shi,amma duk da haka a ƙarshe sai da ƴar ƙwalla ta zubo ma shi jin an ɗaura aure amma ba da shi ba.

Wani irin sanyi mai game da dadɗi ne ya luluɓe William wanda yanzu aka maida mashi suna Mohammed,hannun Khalil ya kama cikin cool voice yace "ka sanyawa ranka dama ba matar ka ba ce,ina mai baka haƙuri duk da wannan shine zaman lafiyar ka dan mother tana iya haukata ka ko kashewa in ka auri Queen "Khalil na jin haka ya ƙyarƙyaro murmushin doli.

Mutane sai barka biyu ake yiwa Mohammed ta aure da musulunta,shi kuma sai wani jin shi yake sama a doli shi ga ango.

***

Zaune take a ɗaki Zee na faman shafa mata dilka a jiki,yayin da ita kuma ta maƙala écouteur da kunne sai waya suke suna hira soyayya ita da Dr.

Cikin shagwaɓa tace "Please ka kashe har mu gama,dilka fah ake shafa min a jiki"Laila ta faɗa kamar zata yi kuka don tunda bikin su ya rage sati biyu Dr ya sha mata kai da kiraye-kirayen waya,zaro ido yayi yace "ga jikiii?ga jiki fa kika ce?wane dan karanbani ne yake aikata wannan kuskuren?"turo baki gaba tayi tace "Zee fah ce kuma ai na ga ba wani abu ba ne tunda mace ce ƴar uwata"numfashi ya sauke cike da tsantsar kishi yace "Please kice mata ta rufe idonta kar ta kalle min ke tunda ba ita ta biya min kuɗin sadakin ba"dariya Laila ta yi kafin ta tsinke kiran.

Yadda suka yi da Dr Laila ta gayawa Zee,dariya tayi tace "eh lalle samun wuri ai sai kice taimaka mashi ne nayi dan fatar jikin ki tayi laushi"cewar Zee tana mai wanke hannunta a roba

dan har ta gama shafa mata.

"Rabu da shi ni wlh har mamakin shi nake sam yanzu bai jin kunyata ba kamar da ba"jan baki Zee tayi tace "ai gwara hakan domin kun kusa zama ɗaya"

NUR POV.

Sosai jikin shi ya fara yin dama tun ranar farko ɗin da aka kai shi asibiti.
Maman ce ta shigo hannunta riƙe da ɗan ƙaramin kwandon abinci,sallama tayi Nuratu wadda ta kasance ƙanwar Nur ta amsa tana mai cewa "maman albishirin ki?"da fara'a tace "goro mi ya faru?"rungume uwar tayi tace "Nur yayi magana kuma har tashi yayi ya shiga douche dan karambani sai da ya so yin wanka nace ya bari har a tambayi likita".

"Da gaske Nuratu?ko dai dan ki kwantar min da hankali ne?"maman ta faɗa tana ƙarasawa bakin gadon da Nur ke kwance ta tsura mashi ido.
"Allah da gaske nake maman bari Dr ya shigo ki ji da bakin shi,dan da kanshi ya ce ya bari har a gama sa mashi allura ruwa tunda lokacin sakata yayi allaso daga baya yayi wankan"cewar Nuratu tana mai son tabbatarwa maman gaskiya ta faɗa mata.

Hamdallah maman tayi kafin ta shiga shafa fuskar tilon yaron nata,Nuratu ma ƙarasowa tayi ta kafe Nur da ido tana jin hutar son shi na ƙara ruruwa a zuciyarta.

Bayan sallah Zuhur Nur ya farka tare da salati bakin shi, ƙoƙarin miƙewa zaune yake nan daddy ya taimaka mashi ya jinginar da shi a pilow.

Kallon su ya tsaya yi ɗaya bayan ɗaya kafin ya rufe ido yana sauke ajiyar zuciya,yanzu ne ya tabbatarwa kanshi tabbas babu abin da ya kai dangi daɗi.

Buɗe ido yayi jin hannun mahaifiyar shi kan fuskar shi tana goge mashi hawayen da ke zuba, "miye kuma na kuka bayan sauƙi ya fara samuwa?ai godiya za ka yiwa Ubangiji"faɗawa yayi jikin maman tare da fashewa da kuka mai ƙarfi "maman sam ban kyauta maku ba kun bani tarbiyya amman na yi fatali da ita,baku rage ni da komi ba am...."kukan da yaci ƙarfin shi ne ya hana shi ƙarasawa,iyayen shi na rarrashinsa yayin da Nuratu ke kuka biyu na murna da na baƙin cikin ganin abun ƙaunarta cikin damuwa.

Da kyar Nur ya yi shiru sannan ya shiga toilet yayi bruch da wanka,sabbin kaya ya saka. Nuratu da kanta ta shiga bashi salade na fruits a baki,sai da ya ci sosai wanda rabin hankalin shi na kanta sai kallonta yake yana mamakin yadda ta girma cikin lokaci ƙanƙane .........
[20/10 à 19:53] MRS SADAUKI 💫: *MUTUM DA RIGAR ALJAN*👹

*Gajeren labari...*
Story
and
Written by
*MRS SADAUKI*
{Cham rose💞}
Dedicated to *PRINCESS AYSHATOU*

☀️ *FIRST CLASS WRITTERS ASSOCIATIONS*☀️

BISMILLAHI RAHMANI RAHIM.

34-35

Tun lokacin da William ya dawo duniyar bil'adama komi na shi ya canza,a baya ya kasance shiru-shiru saboda mother kawai ya sani saɓanin yanzu da ya kasance mai surutu.

Cikin hanzari ya fito daga ɗakin da ya kasance an bashi,hannun shi riƙe da tapis zai je masallacin juma'a.
Tun da ya fito take satar kallon shi ganin yau kyawun da yayi na daban ne duk da cewa dama shi ɗin kyakyawa ne.Caraf idon su ya harɗe cikin na juna,sadda kai ƙasa Maryam ta yi ta na mai jin kunya kamata da yayi tana kallon shi.

Rumtse ido ta yi numfashinta na fita ɗaya-ɗaya yayin da gudun zuciyarta ya ƙaru a sa'ilin da ya zo daf da ita, murmushi yayi yace "Assalamu alaiki amaryar Md da fatan kin wayi garin yau lafiya?"saurin ɗagowa ta yi jin kalaman shi sam ba ta zaci zai yi mata magana ba kasancewar yadda auren su ya zo da sarƙaƙiya bai sa sun keɓe ba ko yin wata hira.

Duƙawa yayi ya hura mata iskan bakin shi kan fuskarta,firgigit ta dawo daidai tare ɗan turo baki gaba shi kuma yayi saurin caɓe laɓanta duk biyun ya shiga kissing.

Sakinta yayi ya na maida numfashi kafin ya zuba mata idanun shi uwanda suka canza kala,kai ƙasa Maryam ta fara wasa da zoben hannunta tana mai jin wani farin ciki.

"Amarya Md kiyi min magana ko na kai ki ɗaki" cewar William dan ya ga a ɗaɗare take,jin haka yasa Maryam ta yunƙura da ƙarfi zata guduwa ɗaki sai aka yi rashin sa'a tayi tuntuɓe ta faɗa jikin shi.

Wata sanyayar ajiyar zuciya suka sauke a tare,luf ta lafe a jikin shi tana jin wata natsuwa na shigar ta.Ƙuguntа ya zagaye da hannuwan shi,kafin ya sauko da kanshi wajen wuyanta daidai saitin kunnenta yayi mata raɗa.Da sauri ta jimƙe ido tana mai ɓoye fuskarta cikin ƙirjin shi,"Please baby ki sake ni kar na rasa jam'i,am...kin ga sai na sake alwala"maƙe kafaɗa tayi alamar ta ƙiya hakan yasa William ciciɓarta ya nufi ɗakinta da ita,kan bed ya direta tare da kwantowa yayi mata rumfa.

Tsura mata ido yayi ganin yadda ƙirjinta ke yin ƙasa da bisa wanda hakan ya kasance na fargaba ne,ta ƙasa t-shirt ɗin ta ya zura hannu ya fara yi mata tafiyar tsutsa har ya kai sama.

Hannun shi ta riƙe tana mai jan numfashi gabanin ta girgiza mashi,cikin rarabewa tace "lok..acin sallah y..ayiii"jin haka William ya mirgina gefe yana mai jin wani abu na tsarga ma shi tun daga kwanya har tafin ƙafa.

Yana fita Maryam ta miƙe zaune tare da dafe zuciya kafin ta saki wani ƙayatacen murmushi lokaci guda kuma ya ɗauke tuna irin halin da ta tarar da momy jiya da suka kai mata ziyara,duk ta jeme tayi baƙi.
Ganin tunanin momy babu abin da zai haifar mata sai tarin damuwa yasa ta shige toilet ta ɗauro alwala tare da gabatar da sallah.

★Bayan sallah isha'i,duka famyling sun haɗu a falo Hajiya Turai (kakar su Maryam)tayi gyaran murya kafin tace "salihu ya kamata fah a fara shirye-shiryen tarewa ƴaƴan nan,tunda komi ya riga da ya lafa ko ya ka gani?"gyara zama dady yayi yace "dama tuni na sa a gyara gidan da na siya kwanaki yanzu haka an gama komi har penti,gobe in Allah ya kai mu sai ayi jere"
"A toh gwara dai haka,ni ma gobe zan koma gidana"Hajiya ta faɗa tana mai tashi tayi masu sai da safe kasancewar tun wuri take kwantawa.

Mohammed dady ya kalla wanda kan shi ke duƙe tunda Hajiya ta fara magana,"Md in akwai abin da kake da buƙata ka sanar da ni kaji ko?"kai William ya daga shi kuma dady ya tashi ya bar wajen sai ya rage daga shi sai Maryam.

Turo baki gaba tayi tace "Ni abar kallona tunda ba tv ba ce"dariya Md yayi wadda ta fito da tsantsar kyawun shi kafin yace "ya aka yi kika san ina kallon ki in ba dai kema kallon nawa kike ba?"
"A'a ni ban kalle ka ba,jikina dai ya bani"Maryam ta faɗa tana mai kallon shi cikin ido.

Sun daɗe suna kallon juna kafin ya sauke ajiyar zuciya yace "mi kika yi min tanadi gobe?"kawar da kai tayi sannan ta amsa da "mi za ayi goben?"waro ido yayi yace "au!baki sani ba?gobe daren farkonmu mana"murmushin gefen baki tayi tace "to miye na sauri ka jira har goben mana,ai surprise ne"da sauri ya taso daga inda ya ke ya zauna kusa da ita yana mai tambayar ta "haba?ki bari Dan Manzo,ashe akwai didima"ɗagowa tayi tana kallon shi cike da mamaki yadda ya iya Hausa har haka.

Gira ya ɗaga mata "yaa miye na kallona?"
"Barci nake ji"ta bashi amsa "ok muje na raka ki"Md ya faɗa yana mai jan hannunta izuwa room ɗin ta.

Washe gari
Tun safe aka shiga gyaran ɗakin amarya,dangin uwa da na uba duk an taru sai hira ake wacce rabinta duk jajen abin da momy ta aikata ne.

Nasiha mai ratsa jiki iyaye suka yi ma ango da amarya kafin a kaita ɗakinta, Mohammed ya samu rakiya Khalil wanda ya koma tun falo yayi masu fatan alkairi.

Hamdallah yayi ga Ubangiji ganin irin ni'imar da yayi mashi lokaci guda,sallama yayi amman bata amsa ba sai gwanjin kuka da take.Bed ɗin ya hau ya jawo ta jikin shi ya shiga aikin rarrashi daƙyar ya shawo kanta har suka yi alwala suka yi sallah suka ci abinci da jus.

Daren farko mai cike da ni'ima hakan ya kasance ga wannan masoyan biyu,sun nuna ma junan su soyayyar zahiri saɓanin wacce suke yi ta mafarki.

Wani irin kuka ne ya zo ma Maryam lokaci guda sa'ilin da taji Md na raɗa mata addu'a kasancewa da iyali,murya na rawa tace "a'a ban so Please ka bari ina jin tsoro ne"

"Innalillahi wa'inna ileyhi raji'un, Please William kar kayi wlh ban so tsoro nake ji"muryar Maryam ke faɗa cikin kuka,ɗago jajayen idanun shi yayi yana kallonta cikin murya ta irin ki tausaya min

yace "ayya babyna ki haƙuri mu raya daren nan kin kau san lokacin da na ɗauka ina jiran wannan ranar?miyasa baki so alhalin burin masoya shine wannan?"kai kawai ta iya girgiza mashi tana son ya ɗagata sai yunƙurin tashi take,cak ta tsaya jin William na kuka kamar wani ƙaramin yaro yana mata magiya zuciyar ta ce ta tsinke da lamarin shi hakan yasa ta ƙanƙame shi gam,shi kuma ya kwararo addu'a yana mai zuwa wajen cikar burin shi duk yadda ya so ya bita a sannu gagara yayi jin shi wani fagen rayuwa inda bai taɓa zuwa ba.

Bayan komi ya lafa ya jawo ta jikin shi suna sauke ajiyar zuciya,kamin ya shiga sa mata albarka da dadaɗen kalamai masu tsayawa a rai.....

***

Baka jin komi sai kukan Laila gefe guda kuma mata sai rangaɗa buɗa suke,cikin kuka take riƙe ƙafafun umma tana jin kamar kar su rabu yayin da kuma wasu mata biyu ke ƙoƙarin miƙar da ita tsaye dan tuni ƴan daukar amarya suke jira.

